# Sanarwar Tsare-tsaren Kariya

Janairu 2025



THE TEXAS LEGAL FRAMEWORK

FW.ESCAPPS.NET

TEA Texas Education Agency

TEA.TEXAS.GOV/TEXASSPED

SPEDTEX Special Education Information Center

SPEDTEX.ORG

# Abubuwan da ke ciki

Sanarwar Tsare-tsaren Kariya....1
Haƙkin Iyayen Yara Masu Fama da Lalura....1
Tsare-tsaren Kariya a Ilmi na Musamman....1
Iyayen goyo a matsayin iyaye....1
Iyayen Goyo....1
Gano Yaro....2
Rubutacciyar Sanarwar Farko....2
Amincewar Iyaye....3
Tsare-tsare A yayin horas da Yara Masu Fama da Lalura....5
Gurabun Sa Kai Na Makaranta Mai Zaman Kanta Na Iyaye....12
Miƙa Haƙƙokin Iyaye....13
Bayanan Ilmi Na Musamman....13
Sulhunta Ɓaraka....13
Gudanar Da Tsarin IEP Na Jaha....14
Ayyukan Shiga Tsakani....14
Shirin Shigar Da Koke Na Ilmi Na Musamman....15
Kyakkyawan Shiri Tsare-tsare....17
Bayanan Tuntuɓa....25
Bayanan tuntubar Sashen Sulhunta Jayayya....25

**SPEDTex babbar albarka ne ga iyalai!**

Tuntuɓi SPEDTex, Cibiyar Bayanin Ilimi ta Musamman.

SPEDTEX Special Education Information Center

www.spedtex.org | 1.855.773.3839

**Haƙkin Mallaka © 2025. Hukumar Ilmi ta Texas. An Mallaki Duk Haƙkin Mallaka.**

# Sanarwar Tsare-tsaren Kariya

# Haƙƙin Iyayen Yara Masu Fama da Lalura

Dokar Ilmi da ta shafi Mutane masu fama da Lalura (**IDEA**) kamar yadda aka yi mata gyara a 2004, ta buƙaci makarantu su samar wa iyayen yaro mai fama da lalura wata sanarwa mai ƙunshe da Tsare-tsaren kariya da ke akwai a ƙarƙashin tsarin IDEA da zartarda ƙa'idojinta. Wannan kundin, da Hukumar Ilmi ta Texas (**TEA**) ta samar, na da manufar cimma buƙatun wannan sanarwa sannan ya taimaki iyayen yaran da ke fama da lalura ya kuma fahimci haƙƙokinsa a ƙarƙashin tsarin IDEA.

## Tsare-tsaren Kariya a Ilmi na Musamman

A ƙarƙashin tsarin IDEA, kalmar mahaifi na nufin mahaifi na jini, iyaye masu riƙo, iyayen goyo waɗanda suka cika sharuɗɗa, mai lura, wani mutum mai matsayin mahaifi na jini ko iyayen riƙo ciki har da kakanni, ƙannen iyaye, ko wani dangi da ke zama tare da yaro, wani mutum mai alhakin kula da walwalar yaro, ko magabatan iyaye.

Kalmar harshen uwa idan aka yi amfani da ita ga wani da ba ya jin harshen Ingilshi sosai na nufin harshen da a bisa al'ada mutumin ke amfani da shi. Idan aka yi amfani da shi ga kurame kuma ko masu lalurar ji, harshen uwa na nufin hanyar isar da saƙo da a bisa al'ada mutumin ke amfani da shi.

A kan buƙaci makaranta ta ba ka wannan Sanarwar Tsare-tsaren Kariya sau daya kawai na shekarar karatu, sai dai dole makaranta ta ba ka wani kwafi na kundin: a bisa turawar farko ko idan ka nemi tantancewa; a bisa buƙatarka na samun koken farko game da ilmi na musamman da aka shigar a TEA; bayan samun sauraren bahaasi na koke a shekarar karatu; lokacin da aka yanke hukunci ladabtarwa da ya ƙunshi sauyin gurbin karatu; a bisa buƙatarka.

Kai da makaranta kun yanke shawara gane da shirin ilmin yaronka ta hanyar samun shiga makaranta, bita, da kora kwamitin (**ARD**). Kwamitin ARD kan duba fahimtar ko yaronka ya cancanci samun ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa. Kwamitin ARD ya samar da, bita, da sake duba kebantaccen tsarin ilmin yaronka (**IEP**) sannan a fahimci sha'anin gurbin karatun yaronka. Akwai ƙarin bayani daga makarantarka a cikin wani kundi akan aikin kwamitin ARD da IDEA [*Jagorar Iyaye ga samun Shiga, Bita, da Sha'anin Sallama*](Publications | Legal Framework (escapps.net)) (Kafa: Publications | Legal Framework (escapps.net)).

## Iyayen goyo a matsayin iyaye

A ƙarƙashin tsarin IDEA, iyayen goyo na iya zama kamar iyaye sai idan dokar jaha ko ƙa'ida ta haramta shi ko wani wajibci daga jaha ko haramcin cikin gida da ya hana iyayen goyo su zma iyaye na jini. A Texas, idan kai uban goyo ne ga yaro mai fama da lalura, kana iya zama a matsayin uba na jini idan ka amince ka shiga tsarin zartaswa na ilmi na musamman sannan idan ka samu horon da ake buƙata kafin taron kwamiti na gaba game da yaron, amma kada ya kasa kwana 90 bayan ka soma zama a matsayin uba na jini don yanke hukunci game da ilmi na musamman ga yaron. Da zarar ka kammala samun horon da aka yarda da shi, ba ka buƙatar sake samun wani horo don zama matsayin uba na jini ga yaron ko kasancewa matsayin uba ko uban riƙo ga wani yaro. Idan makaranta ta yanke shawarar kada a bayyana ka a matsayin uba na jini a kan dalilin yanke hukunci kan ilmi na musamman, dole ne ta ba ka sanarwa a rubuce cikin kwanakin kalanda bakwai bayan ranar da aka yanke hukuncin. Dole ne sanarwar ta bayyana dalilan hukumar ilmi ta cikin gida (**LEA's**) na matakinta sannan dole a sanar da kai cewa kana iya yin koke a gaban TEA.

## Iyayen Goyo

Idan, bayan wani ƙoƙari, makaranta ba ta iya gano, ko samun uban yaro, iyayen riƙo ba su buƙatar ko ba su iya zama a matsayin iyaye na jini, yaron bai zaune a gidan

iyayen riƙo, ko yaron na a unguwar jaha, to dole ne makaranta ta samar da magabatan iyaye su tsaya a madadin iyayen yaro, sai fa idan yaron na hannun jaha ne kuma kotu ta samar da wani magabacin iyaye. Dole makaranta ta samar da magabatan iyaye ga matashin da bai da gida kamar yadda Dokar McKinney-Vento da ta shafi Taimakon Maras Gida ta bayyana. Da zarar an samar da magabacin uba ga yaron da bai da gida ko an saka shi a kulawa, dole ne makaranta ta samar da sanarwa a rubuce na aikin mai kula da ilmin yaron da ma'aikacin harkar.
Don karin bayani, ziyarci [Yara da Matashin da Ke Fuskantar Rashin Gida (Kafa: bit.ly/39v6KzG)](bit.ly/39v6KzG).

Don cancantar zama magabaci, dole ne ka kada ka zama ma'aikacin TEA, makarantar, ko kowace hukuma da ke cikin sha'anin ilmi ko kula da yaron, sannan dole ne ya zama ba kada wani ra'ayi na daban da abinda yaron ke sha'awa. Wanda aka ba matsayin magabacin dole ne ya zama yana da wadataccen ilmi da gogewa, yana son aikin, yana da ikon kan sa wajen kula da abinda yaron ke sha'awa, tabbatar da cewa ba a dafe haƙƙoƙin yaro ba, ziyartar yaron da makarantar, bitar bayanan makaranta na yaron, tuntuɓar kowane mutum mai alhakin kula da ilmantar da yaron, halartar tarukan kwamitin ARD, kammala shirin bayar da horo. Wanda makaranta ta ba alhakim zama magabacin dole ne ya kammala samun horo kafin taron gaba na kwamitin ARD amma kada ya zama ƙasa da kwana 90 daga ranar da ya soma aikin na zama magabacin. Da zarar ka kammala samun horon da aka yarda da shi, ba ka buƙatar sake samun wani horo don zama matsayin uba na jini ga yaron ko kasancewa matsayin uba ko uban riƙo ga wani yaro.

Don ƙarin wasu ƙa'idoji dangane da magabatan iyaye, sai a duba [19 TAC §89.1047 (Kafa: https://bit.ly/48MJXOa)](https://bit.ly/48MJXOa).

## Gano Yaro

Dukan yara masu lalura da ke zaune a jahar, waɗanda ke da bukatar ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa da shi, wanda ya haɗa da yara masu lalura da ba su da gidajen zama waɗanda ke ƙarƙarshin kulawar gwamnati da yara masu lalura da ke karatu a makarantu masu zaman kansu, ba tare da la'akari da tsanani ko sauƙin lalurarsu ba, to dole ne a bincika, a ganosu sannan a tantace su. Ana kiran wannan mataki da Gano Yaro.

A cikin tsarin ayyukanta na Gano Yaro, dole ne LEA ta wallafa ko bayar da sanarwa a jaridu ko kafar watsa labarai, ko biyu, da suka karaɗe ko'ina su sanarwa iyayen yaro game da ayyukan, bincika, da tantance yaran da ke da buƙatar ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa.

Don samun cikakken bayanin ƙa'idoji game da tsarin Gano Yaro, sai a tuntubi [Tsarin Shari'a Sha'anin Yara Masu Neman Ilmi na Musamman (Kafa: fw.escapps.net)](fw.escapps.net).

## Rubutacciyar Sanarwar Farko

Kana da haƙƙin a ba ka bayani a rubuce game da ayyukan makaranta masu alaƙa da buƙatar yaronka akan ilmi na musamman. Dole ne makaranta ta samar maka sanarwa a rubuce a lokacin da ya dace kafin ta soma ko fito da sauyin hanyar ganewa, tantancewa, ko gurbin karatu yaronka ko samun ilmin jama'a a kyauta (**FAPE**) ga yaronka. Kana kuma da haƙƙi samun sanarwar a rubuce tun farko kafin makarantar ta ƙi soma ko aiwatar da hanyar ganewa, tantancewa, ko samar da gurbin karatu ko tsarin FAPE ga yaronka. Dole makaranta ta samar maka da sanarwa a rubuce duka ko amince da sauyin ko ka nemi a yi sauyin.

A Texas, dole ne tun da farko makaranta ta samar maka da sanarwa a rubuce akalla kwana biyar na karatu kafin zartasshawarar ko ƙin amincewa da matakin sai fa idan ka amince a cikin gajeren lokaci.

Dole tun farko makaranta ta hada da sanarwa a rubuce: bayanin yadda ayyukan da makaranta ke zartarwa ko ke ƙin gudanarwa; a bayanin kowace hanyar tantancewa, kimantawa, adana bayani, ko rahoton da makaranta ta yi amfani da shi wajen zartaswa ko ƙin aikin; bayanin cewa kana da kariya a ƙarƙashin tsare-tsaren kariya na IDEA; bayanain yadda za a samu kwafin wannan Sanarwar Tsare-tsaren Kariya; bayanan

tuntuba ga wasu ko hukumomi da ke iya taimaka maka fahimtar IDEA; cikakken bayanin wasu zabin da kwamitin ARD na yaronka ya yi la'akari da su da dalilan da suka sa aka yi watsai da waɗannan zaɓi; da cikakken bayani wasu dalilan da suka sa makaranta ta zartas ko ƙin matakin.

Dole ne rubutacciyar sanarwar ta kasance a harshen da al'umma ke fahimta sannan dole a fassara ta cikin harshen gida ko wata hanyar isar da saƙo sai fa idan hakan ba zai yuwu ba.

Idan harshenka ko wata hanyar isar da saƙo ba a harshen da ke da rubutu ba ne, to dole ne makaranta ta fassara sanarwar a baka ko ta wasu hanyoyin da harshenka ko hanyar isar da saƙo don ka fahimce shi. Dole makaranta ta samar da hujja a rubuce cewa an yi hakan.

Ko bayan makaranta ta soma samar da ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa da shi ga yaronka, idan ka janye amincewarka a kowane lokXI ga ayyukan, to dole ne makaranta ta dakatar da samar wa yaronka ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa da shi. Saidai kuma, kafin dakatar da ayyukan, dole ne tun da farko makaratar ta ba ka sanarwa a rubuce akalla kwana biyar na zuwa makaranta kafin ayukan su ƙare, sai fa idan ka amince da saka gajeran lokaci.

### Imel na Latironi

Mahaifin yaron da ke fama da lalura na iya neman a tura masa saƙo ta imel na latironi idan makaratar ta samar da wannan dama.

## Amincewar Iyaye

Dole ne makaranta ta nemi amincewarka kafin ta iya yin wani abu daban. Amincewarka da ka sanar na nufin cewa: ka bayar da dukan bayanan da ke da dangantaka da dalilin da ya sa aka nemi izininka a cikin harshenka ko ta wata hanyar isar da saƙo; da ka ke fahimta sannan ka amince a rubuce zuwa ga sashen ayyukan da aka nemi izinin naka, sannan kuma amincewar a rubuce ta bayyana aikin da jerin adanannun bayanai da za a fitar sannan zuwa ga wanda; sannan ka fahimci cewa bayar da amincewarka na ganin dama ne kuma kana iya janyewa a kowane lokaci. Idan kana son ka janye amincewarka ga ci gaba da samar da tanadin ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa, dole ne ka yi a rubuce. Idan ka amince sannan ka janye ta, ba za yarda da janyewarka ba.

Dole ne makaranta ta samar da bayanan da aka ajiye na wata himmar da aka yi wajen samun amincewar mahaifi. Bayan da aka ajiye sun ƙunshi bayanan ƙoƙarin makaranta wajen samun amincewa kamar ajiye lambobin waya, kwafi na abubuwa da suka biyo, da cikakkakun adanannun bayanan ziyarar da aka yi a gidanka ko wurin aiki.

### Tantancewar Farko

Kafin gudanar da tantancewar farko ta yaronka don fahimtar ko yaronka ya cancancta a matsayin mai fama da lalura a ƙarƙashin tsarin IDEA, dole ne makaranta ta ba ka kwafin Tsare-tsaren Sanarwar Kariya, da kwafin fom na Bita kan Ilimi na Musamman Domin Iyaye wanda hukumar TEA ta samar, sannan da rubutacciyar sanarwa shirin tantancewar da aka samar tun da fari sai kuma a samu amincewarka bayan ka fahimci komi. Dole ne makarantar ta yi ƙoƙarin da ya dace dan samun amincewarka don tantancewa a karon farko. Amincewarka don tantancewar farko ba ya nufin cewa ka kuma amince makaranta ta soma samarwa yaronka tsarin ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa. Idan yaronka yana a hannun jaha sannan ba ya zaune tare da kai, to makaranta ba ta buƙatar samun amincewarka idan ba za su iya samun ka ba ko idan an dakatar da ikon haƙƙin iyaye ko kuma kotu ta bayar da umurnin saka wani a mastayin.

### Ayyukan Farko

Dole ne a karon farko makaranta ta samu amincewarka da ka sanar kafin samarwa yaronka ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa. Dole ne a karon farko makaranta ta yi ƙoƙarin samun amincewarka da ka sanar kafin samarwa yaronka ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa. Idan kuma ba ka mayar da amsa ba ga buƙatar samar da amincewarka don yaron ka ya samu ilmi na musamman da ayuka masu alaƙa a karon

farko, ko idan ka ƙi bayar da irin wannan amincewar ko daga baya ka janye (soke) amincewarka a rubuce, mai yiwuwa makarantarka ba za ta yi amfani da tsare-tsaren kariya (wato, shiga tsakani, koke akan tsari, taron sulhu, ko wani sashin sauraren bahaasi ba) don cimma yarjejeniya ko dogara cewa mai yiwuwa a ba ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa da kwamitin ARD ya bayar da shawara ba tare da amincewarka ba.

Idan ka ƙi bayar da amincewarka don yaronka ya samu ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa a karon farko, ko idan ba ka bayar da amsa ba ga buƙatar ka samar da irin wannan amincewar ko daga baya ka janye (soke) amincewarka a rubuce sannan makaranta ba ta samarwa yaronka da ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa ba, da ka nemi amincewarka, to makarantarka ba ta karya doka na buƙatar samarwa yaronka tsarin FAPE saboda kasawarta wajen samar da wadannan ayyuka ga yaronka; sannan ba buƙatar kwamitin ARD ya gudanar da taro ko samar da IEP ga yaronka na ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa da aka nemin amincewarka.

Idan ka janye (soke) amincewarka a rubuce a kowane mataki bayan an samarwa ilmi na musaman da ayyuka masu alaƙa, to makaranta na iya daina ci gaba da samar irin waɗannan ayyuka, amma dole ne a samar maka da sanarwa a rubuce tun farko, kamar yadda aka bayyana a ƙarƙashin taken Rubutacciyar Sanarwar Farko, kafin a dakatar da ci gaba da samar da waɗannan ayyuka.

### Sake tantancewa

Dole makaranta ta samu amincewarka na sake tantance yaronka sai fa idan ta na iya nuna cewa ta ɗauki ƙwararan matakai wajen samun amincewarka sannan ka ƙi bayar da amsa.

Matakan da aka Soke – Idan an saka yaronka a makarantar gwamnati ko kana neman saka yaronka a makarantar gwamnati sannan ka ki samar da amincewarka ko ka kasa bayar da amsa ga buƙatar da aka yi na ka samar da amincewa saboda tantancewar farko, to ka na iya, makarantarka na iya, amma ba buƙaci, neman tantance yaronka ba a matakin farko ta hanyar amfani da tsarin shiga tsakani na IDEA ko yin sauraren bahasi na koke, taron sulhu, da wani wasu hanyoyin gudanar da sauraren bahasin. Makarantarka ba za ta karya dokar wajibcinta na bin sawu, gano, da tantance yaron ka ba (wajibcin gano yaro) idan ba ta gudanar da tantance yaronka a bisa waɗannan sharudda.

Idan ka ƙi amincewa a sake tantance yaronka, makaranta na iya, amma ba a buƙaci, bin dinddigin sake tantance yaronka ta hanyar shiga tsakani, yin koke, taron sulhu, da wasu hanyoyin gudanar da sauraren bahasi don neman watsi da ƙin amincewarka kan sake tantance yaronka. Daga soma tantancewar farko, makarantarka ba za ta karya dokar wajibcinta a ƙarƙashin IDEA idan ba ta soke neman sake tantancewa a wannan tsarin.

Idan mahaifin yaron da ke makaranta cikin gida ko a aka saka a makaranta mai zaman kanta da tallafin iyaye ba yana nufin amincewa da tantancewa ko sake tantancewa ko mahaifi ya kasa bayar da amsa ga buƙatar neman amincewa, to makaranta na iya ƙin amfani da tsarin IDEA na ƙiin amincewa da hanyoyin da aka bayyana a sama. Kuma ba buƙatarh undumar makaranta ta yi la'akari da yaronka a matsayin wanda ya dace ya samu daidaito wajen kulawar (akwai ayyukan a wasu makarantu masu zaman kansu don iyaye masu yara da ke fama da lalura).

Ba a buƙatar amincewarka kafin makaranta ta yi bitar bayanan da ke akwai a wani bangare na tantance yaronka ko sake tantance yaronka ko ba yi ma yaronka jarabawa ko wani nau'in tantancewa da a kan ba dukan yara sai fa idan akwai buƙatar neman izinin iyayen dukan yaran. Makaranta na iya ƙin amfani da amincewarka ga amfani da wani aiki ko hidima don hana maka ko yaronka kowace hidima, amfana, ko aiki.

### Tantancewar Ilmi Mai Zaman Kanta

Tantancewar ilmi mai zaman kanta (**IEE**) tsarin tantancewa ne da wani ƙwararre kan gudanarwa wanda ba ma'aikacin makaranta ba. Kana da haƙƙin samun tantancewar mai zaman kanta IEE ta yaronka idan ba ka amince da tantance yaronka da

makarantarka ta samu ba. Lokacin da ka nemi tantancewar ilmi mai zaman kanta IEE, dole ne makarantar ta ba ka bayanai game da tsarin tantancewarta da inda za a samu IEE.

### IEE a cikin Kuɗaɗen Jama'a

Idan ka ƙi yarda da yin tantancewar da makaranta ta tsara, to kana da haƙƙin neman wani da ba ma'aikacin makarantar ba ya tantance yaronka, a cikin kuɗaɗen jama'a.

Kuɗaɗen jama'a na nufin cewa ko dai makaranta ta biya duk kuɗin tantancewar ko tabbatar da cewa an samar maka da tantancewar a kyauta.

Idan ka nemi IEE na yaronka a cikin kuɗaɗen jama'a, dole ne makarantarka ta, ba tare da wani ɓata lokaci ba, **ko dai:** (a) Shigar da koken a bisa tsari don neman a saurara nuna cewa tsarinta na tantance yaronka ya dace; **ko** (b) Samar da IEE a kuɗaɗen jama'a, face sai idan makaranta ta nuna a wani sauraren bahasi cewa bayanan tantance yaronka da ka samu ba su yi daidai da tsarin makaranta ba.

Ka cancanci samun IEE ɗaya kawai a cikin kuɗin jama'a kowane lokaci makaranta ta gudanar da tantancewar da ba ka amince ba.

Idan ka nemi IEE na yaronka, makaranta na iya tambayar ka dalilin ƙin amincewa bayanan tantance yaronka da makarantarka ta samu. Haka kuma, makarantarka na iya buƙatar bayanai kuma iya kawo tsaiko wajen samar da IEE na yaronka a cikin kuɗaɗen jama'a ba tare da kawo wani dalili ba ko shigar da koken buƙatar sauraren bahasi don goyon bayan makaranta tantance yaronka.

### Tsarin IEE

Idan da kuɗaɗen jama'a IEE yake, tsarin wanda ƙarƙashinsa ake samar da tantancewa, ciki har da gano tsarin tantancewa da ƙwarewar mai tantancewa, kuma dole ne su zama iri ɗaya da tsarin da makaranta kan yi amfani da shi lokacin da ta fara tantancewa gwargwadon yadda waɗannan tsare-tsare suka yi daidai da haƙƙinka ga IEE. Sai fa don ci gaba da tsarin, makaranta na iya ƙin saka sharuɗɗa ko lokacin dangane da samun IEE a kuɗaɗen jama'a.

### Kaddamar Da Jam'in Saurare

Idan makaranta ta saka koken a kan buƙatar gudanar da sauraren bahasi sannan jami'in sauraren ya ƙuduri cewa tantancewar ta makaranta abu ne da ya dace ko cewa IEE da aka samu bai cika sharuɗɗan IEE na makaranta ba, to makaranta ba za ta biya ba wajen samar da IEE ba.

### IEE a cikin Kuɗaɗen Jama'a

Kullu ma kana da haƙƙin samun IEE da kuɗinka. Ko dai waye ya biya aikin, dole ne makaranta ta yi laka'akari da IEE a cikin kowane mataki game samar da FAPE ga yaronka idan har IEE ya cika sharuɗɗan makaranta. Kana kuma iya gabatar da IEE a matsayin hujjar sauraren bahasi.

### IEE da Jami'in Sauraren Bahasi Ya Bada Umurni

Idan jami'in sauraren bahasi ya bayar da umurni kan IEE a matsayin wani sashi na sauraren bahasi, dole ne makaranta ta biya.

## Tsare-tsare A yayin horas da Yara Masu Fama da Lalura

### Ikon Ma'akacin Makaranta

#### Kudurin-Hukunce-Hukuncen Shari'a

Ma'aikacin makaranta na iya la'akari da kowane lamarin bisa tsarin ƙudurin-hukunce-hukunce a yayin neman tantance ko sauyin gurbin karatu, an yi bisa tsari da yayi daidai da waɗannan ƙa'idoji masu dangantaka da ɓangaren, ya dace ga yaro mai lalura da ya karya dokar makaranta na tsarin dokokin ɗalibi.

#### Gabaɗaya

Gwargwadon yadda su ka ɗauki mataki ga yaran da ba su fama da lalura, ma'aikacin makaranta na iya, cikin abin da bai gaza kwana 10 na karatu ba a jere, cire yaron da ke fama da lalura wanda kuma ya karya dokar ɗalibi daga gurbin karatunsa ko gurbin karatunta zuwa

wani tsarin samar da ilmi na (**IAES**), wani tsari, ko kuma dakatarwa. Ma'aikacin makaranta na iya ƙara cire yaro a ciki kwanakin karatu da ba su gaza 10 ba a jere na wannan shekarar karatu a lokuta daba-daban na aikata rashin ɗa'a, muddin dai cirewar ba ta haddasa sauyin gurbi (duba take Samar da Gurbi Saboda Cirewa Don Ladabtarwa ga ma'anar). Da zarar aka cire yaron da ke fama da lalura da gurbin karatunsa ko gurbin karatunta na yanzu tsawon jimillar kwana 10 na karatu a wannan shekarar karatun, to dole ne makaranta, a lokacin kwanakin da a ka ciren da ke tafe a wannan shekarar karatu, samar da ayyuka gwargwadon yadda aka nema a ƙarƙashin babban-take Ayyuka.

**Karin Iko**

Idan halin da ya haddasa karya dokar dalibi ba wata bayyananiyar lalurar yaro ba ce, to tsarin ladabtarwa kan sauyin gurbin zai zarce kwana 10 na karatu a jere, ma'aikacin makaranta na iya fito da hanyoyin ladabtar da yaron da ke da lalura a tsari iri daya na wannan tsawon lokacin kamar dai yadda ya ke ga ɗaliban da ba su fama da lalura, sai fa idan ya zama dole makaranta ta samar da hidima ga yaron kamar yadda aka bayyana a ƙarƙashin Ayyuka. Kwamitin yaro na ARD kan ƙuduri tsarin IAES ga irin waɗannan ayyuka.

**Ayyuka**

Ba bukatar gundumar makaranta ne ba ta samar da ayyukan ga yaro mai fama da lalura idan akan cire shi daga gurbinsa ko gurbinta na yanzu tsawon kwana 10 a jere ko kasa da haka a shekarar karatu idan ba ta samar da kulawa ga yaron da ba shi fama da lalura. Yaron da ke fama da lalura da aka cire daga gurbin karatu fiye da kwana 10 na karatu kuma dabi'ar ba ta da dangantaka da lalurar yaron ko wanda aka cire a bisa wasu dalilai to dole ne:

- Ci gaba da samun ayyukan ilmi (da ke akwai a FAPE), don ba yaro damar ci gaba da shiga cikin manhajar tsarin ilmin bai daya, duk da yake a wani tsari (da watakila zai iya zama IAES), sannan da ci gaba don cimma burukan da aka saka a IEP na yaro; da
- Karɓa, kamar yadda ya dace, kimanta tsarin ɗabi'a mai aiki, da ayyukan shiga tsakani, da sauye-sauye, da aka tsara don magance matsalar rashin ɗa'a sai a kange ta daga faruwa nan gaba.

Bayan an cire yaro mai lalur daga gurbin karatunsa ko gurbin karatunta na yanzu na tsawon kwana 10 na karatu a wannan shekarar karatu, sannan idan cirewar ta yanzu ta tsawon kwana 10 ce a jere ko ƙasa da haka sannan idan cirewar ba sauyi ce ga gurbin karatu ba (duba bayani a ƙasa), to ma'aikacin makarantar, a cikin tuntuɓar da ake da aƙalla ɗaya daga malamin yaron, ya ƙudurci cewa gwargwadon ayukan da ake buƙata don ba yaro damar ci gaba da shiga tsarin manhajar ilmin bai ɗaya, duk da yake a wani tsarin, sannan da ci gaba don cimma burukan da aka saka a IEP na yaron.

Idan cirewar sauyi ce ga gurbin karatu, to kwamitin ARD na yaro kan ƙudurta ayyukan da suka dace don ba yaro damar ci gaba da shiga cikin manhajar tsarin ilmin bai daya, duk da yake a wani tsari (da watakila zai iya zama IAES), sannan da ci gaba don cimma burukan da aka saka a IEP na yaro.

**Bayyanannen Kuduri**

Cikin kwana 10 na karatu kowane matakin sauya gurbin karatun yaro mai lalura saboda karya dokar da ta shafi dalibai (in ban da cirewar da ta kai tsawon kwana 10 a jere ko ƙasa da haka kuma ba sauyi ba ne ga gurbin karatun), makarantar, kai, da memebobi masu alaƙa da juna na kwamitin ARD (kamar yadda kai da makaranta kuka tsara) dole ne a yi bitar duk bayanai masu alaƙa a fayil na ɗalibi, ciki har da IEP na yaron, shawarar kowane malami, da kowane bayani mai alaƙa da ka samar don yanke hukunci:

- Idan halin da ake tababa ya faru saboda, ko ya yana nuna alaƙa ta kai tsaye zuwa ga, lalurar da yaronka ke fama da ita; ko
- Idan halin da ake tababa kai tsaye ya faru ne saboda kasawar makarantar don aiwatar da IEP na yaron ne.

Idan makarantar, kai, da wasu membobi masu alaƙa na kwamitin ARD na yaron suka ƙudurta cewa ba wani daga saharuɗɗan biyu da aka cimma, to dole ne yadda cewa halin da ya faru na da alaƙa da lalular da yaron ke fama da ita.

Idan makarantar, kai, da wasu membobi masu alaƙa da kwamitin ARD na yaron suka ƙudurta cewa halin da ya faru da ake tababa na da nasaba ta kai tsaye da kasawar makaranta wajen aiwatar da IEP, to dole ne makarantar ta ɗauki matakin cikin gaggawa don magance wannan gazawar.

**Kudurta cewa Halin na da nasaba da Bayyananniyar Lalurar Yaro**

Ida makarantar, kai, da wasu membobi masu alaƙa da kwamitin ARD na yaro suka ƙudurta cewa halin na da nasaba da bayyananniyar lalurar yaron, to dole kwamitin ARD ya ko dai:

- A gudanar da kimanta yadda halayya ta ke, sai fa idan makaranta ta riga ta gudanar da kimanta yadda halayya ta ke kafiin halin da ya kai ga sauya gurbin karatu ya faru, sannan a aiwatar da shirin shiga tsakani don lura da halayyar yaro; ko
- Idan an riga an samar da shirin shiga tsakani don lura da halayyar yaro, yi bitar shirin shiga tsakani don lura da halayyar yaro, sannan a sauya, yadda ya dace, don a magance matsalar da ta shafi halayya.

Sai fa kamar yadda aka bayyana ne a sashe Muhimman Lamurra, dole ne makaranta ta dawo da yaronka zuwa ga gurbin karatun da aka cire shi, sai fa idan ko da gunduma kun cimma matsayar sauya gurbin karatun a matsayin wani ɓangaren na sauyin shirin shiga tsakani don lura da halayya.

**Muhimman Lamurra**

Ko kuwa wani hali ne ya bayyana dangane da lalurar yaronka, mai yiwuwa wani jami'in makaranta na iya cire ɗalibin zuwa IEAS (yadda kwamitin ARD na yaron ya tsara), kada ya zarce kwanakin karatu 45, idan har yaronka:

- Kan ɗauki makami (duba bayanin da ke ƙasa) ko ya mallaki makami a makaranta, ko harabar makaranta, ko a lokacin da ake karatu a ƙarƙashin hukuncin TEA ko makaranta;
- A bisa sani yana da ko amfani da haramtattun ƙwayoyi (duba bayanin a ƙasa), ko sayar da ko shiga cinikin abubuwan da aka hana, (duba bayanin da ke ƙasa), lokcin da ya ke makaranta, a harabar makaranta, ko lokacin da ake karatu a ƙarƙashin hukuncin TEA ko makaranta; ko
- Ya yi ma wani mummunan rauni a jiki (duba bayanin da ke ƙasa) kai ma wani farmaki a makaranta, ko harabar makaranta, ko a lokacin da ake karatu a ƙarƙashin hukuncin TEA ko makaranta.

**Bayani**

**Abubuwan da aka hana amfani da su** na nufin ƙwaya ko wani abu da aka bayyana a ƙarƙashin tsarin I, II, III, IV, or V ia Sashi 202(c) Dokar Haramta Miyagun Abubuwa (21 U.S.C. 812(c)).

**Haramtattun ƙwayoyi** na nufin abubuwan da aka hana amfani da su, amma ba su ƙunshi abubuwan da aka hana da aka samu izinin mallakar su ba ko ke ƙarƙashin kulawar ƙwararren jami'in kiyon lafiya mai lasisi ko da aka mallaka bisa doka ko wata hukuma ke amfani da su a ƙarƙashin kowane tsarin sa ido na Dokar tarayya.

**Mummunan rauni a jiki** na da ma'anar da aka ba mummunan rauni a jiki a cikin sakin layi na (3) na ƙaramin sashi na (h) Sashe na1365 mai Taken 18, na Dokar Amurka.

**Makami** na da ma'anar da aka ba kalmar makami mai haɗari a cikin sakin layi na (2) na ƙaramin sashi na farko na (g) Sashi na 930 mai Taken 18, na Dokar Amurka.

**Sanarwa**

A ranar da ta yanke shawarar cirewar wannan shi zai zama sauyin matsayin yaronka domin keta dokar ɗabi'ar yaro, dole ne gundumar makaranta ta sanar da kai game da wannan mataki, ta kuma samar maka da sanarwar tsare-tsaren kariya.

### Sauyin Gurbi don Cirewar Ladabtarwa

Cire yaronka maii fama da lalura daga gurbin yaronka sauyin gurbin karatu ne idan:

- Cirewar ta zarta kwana 10 na karatu a jere; ko
- Yaronka ya fuskanci cirewa barkatai da ta haddasa abubuwa saboda:
    - Jerin adadin kwana 10 na karatu na cirewar a shekarar karatu;
    - Halayar yaronka ta fi kama da halayyar yaro a lokacin abubuwan da suka faru a baya da suka haddasa yawan jerin cirewar; sannan
    - Wasu abubuwa kamar tsawon lokacin cirewar, adadin lokacin da aka cire yaro, da kusancin tsakanin wata cirewar da wata.

Ko dai zubin cirewar ya haddasa sauyin gurbin karatu ya ta'allaka a bisa ƙudurin-hukunce-hukunce na makaranta sannan, idan an ƙalubalance shi, akwai yiwuwar sake bitarsa ta hanyar sauraren bahasi da zaman shari'a.

### Kaddamar Da Shiri

Kwamitin ARD kan yanke shekarar amfani da IEAS don cirewar da za ta shafi gurbin karatu, da cirewar da ta shafi sassan Karin Iko da Al'amurra na Musamman.

### Ɗaukaka ƙara

#### Gabaɗaya

Kana iya shigar da koken sauraren bahasi don neman sauraren bahasi idan ba ka amince da:

- Kowane mataki da ya shafi gurbi da aka ɗauka a ƙarƙashin waɗannan tanade-tanaden ladartarwa; ko
- Bayyanannen ƙudurin da aka bayyana a sama.

Makaranta na iya shigar da koken sauraren bahasi don neman sauraren bahasin idan ta yarda cewa ci gaba da kare gurbin yaronka na yanzu na iya haddasa rauni sosai ga yaronka ko ga wasu.

#### Karfin Ikon Jami'in Sauraren Bahasi

Jami'i da ke sauraren bahasi da ya cika sharuɗɗan da aka ambata a sashen Tsare-tsaren sauraren bahasi a ƙasa dole ne ya aiwatar da sauraren bahasin sannan ya yanke hukunci. Jami'in sauraren bahasi na iya:

- Mayar da yaronka mai fama da lalura zuwa ga gurbin da aka cire yaronka ida jami'in sauraren bahasin ya yanken shawarar cewa cirewa ta saɓawa sharuɗɗan da aka ambata a ƙarƙashin taken Ikon Jam'in Makaranta, ko cewa halayyar yaronka na da alaƙa da lalurar da yaronka ke fama da ita; ko
- Bayar da umurnin sauya gurbin karatun yaronka mai lalura zuwa ga tsarin IEAS da ya dace kada ya zarce kwana 45 na lokacin karatu idan har jami'in sauraren bahasin ya yanke shawarar cewa ci gaba da kare gurbin yaronka na iya haddasa rauni sosai ga yaronka ko ga wasu.

Ana iya maimaita waɗannan tsare-tsaren sauraren bahasi, idan har makaranta ta yarda cewa dawowar yaronka ga gurbinsa na ainihi na iya haddasa rauni sosai ga yaronka ko wasu.

A koyaushe kai ko makaranta kuka saka koke don gudanar da sauraren bahasi, to dole ne a gudanar da wanda ya cika sharuɗɗan da aka ambata a sashen Tsare-tsaren da aka Tanada a ƙasa, ai dai kamar haka:

- Dole ne TEA ko makaranta su shirya don sauraren bahasi na gaba, wanda dole ya gudana cikin kwanakin karau 20 na ranar sauraren bahasi da aka nema sannan dole ne ya bayyana ƙudurin a cikin kwana 10 na karatu bayan saurare.
- Har sai kai da makarantar kun amince a rubuce ku bar gudanar da taron, ko yarda ku yi amfani da tsarin shiga tsakanin, dole ne taron sulhun ya wakana cikin kwana bakwai na kalanda daga samun koke game da sauraren bahasi. Sauraren bahasin zai ci gaba sai fa idan an sulhunta batun ya kuma gamsar da sassan biyu a cikin kwanakin kalanda 15 na samun koke game da saurare.

- Jaha na iya samar da tsare-tsare don shirin sauraren bahasin fiye da yadda aka samar da su ga wani shirin sauraren bahasi, amma face sai don lokacin da aka shata, dole ne waɗancan dokoki su dace da dokokin a wannan kundi dangane da lamarin sauraren.

Kai ko makarantar na iya ɗaukaka matakin a cikin sauraren bahasin da ake jira iri ɗaya da matakai a cikin wani shirin sauraren bahasi, kamar yadda aka bayyana a ƙasa cikin sashen Ayyukan Fararen Hula.

#### Samar da Gurbi Lokacin Roƙo

Yayin da, kamar yadda aka bayyana a sama, kai ko makarantar kuka saka koken mai alaƙa da sha'anin ladabtarwa, dole ne yaronka, (sai fa idan kai da TEA ko makarantar kun yarda da akasin haka) ci gaba da jiran matakin jami'in sauraren bahasi, ko har sai lokacin da aka shata na cirewar ya wuce don sannan aka bayyana a ƙarƙashin taken Ikon Jami'in Makaranta, duk dai wanda ya fara aukuwa.

### Kariyar Yara Bai Dace Ba Yanzu Ga Ilmi Na Musamman Da Ayyuka Masu Alaƙa

#### Gabaɗaya

Idan ba a kai ga tabbatar da cancantar yaronka ga samun ilmi na musamman da ayuka masu alaƙa ba sannan ya karya dokar dalibi, amma makarantar na da masaniyar haka (kamar yadda aka yi hasashe a ƙasa) kafin halayyar da ta haddasa ɗaukar matakin ladabtar da ta faru cewa yaronka na da lalura, sannan yaronka na iya bayyana kowace irin kariya da aka bayyana cikin wannan kundi.

#### Hujjojin Da aka Dogara Da Su Wajen Ladabtarwa

Makaranta za ta san da cewa yaronka na fama da lalura idan, kafin lokacin da halin ya haddasa daukar matakin ladabtarwa ya auku:

- Ka nuna damuwa a rubuce zuwa mai lura ko wani jami'in sashen mulki na wata fitacciyar hukumar ilmi, ko zuwa ga malamin yaronka cewa yaronka na da buƙatar ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa;
- Ka nemi tantancewa dangane da cancantar samun ilmi na musmman da ayyuka masu alaƙa a ƙarƙashin IDEA Kashi na B; ko
- Malamin yaronka ko wani jami'in makaranta ya bayyana takamaiman damuwa game da tarin halayen da yaronka ya nuna kai tsaye ga daraktan makaranta na ilmi na musamman ko wani jami'in makarantar da ke saka ido.

*In ban da* – Makaranta ba za ta san da wannan lamari ba idan:

- Ba ka bayar da tantance yaronka ba ko ka ki yarda da ayyuka na musamman; ko
- An tantance yaronka sannan an lura yaro ne da ba shi fama da lalura a ƙarƙashin IDEA Sashe B.

#### Sharuddan da suka Shafi idan akwai Rashin Tabbaci

Idan kafin daukan matakin ladabtarwa a kan yaronka, makaranta ba ta da masaniya cewa yaronka yaro ne mai fama da lalura kamar yadda aka bayyana a sama a Tabbaci Don Lamurran Ladab tarwa da Na Daban, yaronka na iya iya fuskantar matakan ladabtarwa da suka shafi yaran da ba su fama da lalura da suka aikata halayya iri guda. Haka kuma, idan an nemi a tantance yaronka a lokacin da yaronka ya fusanci matakin ladabtarwa, dole ne a gudanar da tantancewar cikin hanzari. Har zuwa kammala tantancewar, yaronka zai ci gaba da zama a gurbin samar da ilmin kamar yadda mahukunta makaranta suka yanke shawara, da zai iya haɗawa da dakatarwa, ko kora ba tare da samun ayyukan ilmin ba. Idan an yanke hukuncin cewa yaronka na fama da lalura, yin la'akari da bayanan daga tantancewar da makaranta ta gudanar da bayanan da ka samar, dole ne makaranta ta samar da ilmi na musamman d ayyuka masu alaƙa a bisa tsarin IDE Kashi na B, ciki kuwa har da sharuɗɗan ladabtarwa da aka ambata a sama.

#### Turawa zuwa da Matakin Masu Tilasta Bin Doka da Alƙalai

Sashin B na IDEA ba shi:

- Haramta hukuma daga kai rahoto ga mahukunta kan babban laifin da yaro mai lalura ya aikata; ko

- Hana masu tilasta bin doka na Texa da alƙalai samun haƙƙoƙinsu dangane da aikace-aikacen masu tilasta bin doka da dokar jaha game da laifukan da yaron da ke fama da lalura ya aikata.

**Bayanan da ake iya Watsawa**

Idan makaranta ta bayar da rahoton laifin da yaro mai lalura ya aikata, makarantar:

- Dole a tabbatar da cewa kwafi-kwafi na bayanan ilmi na musamman na yaro da bayanan ladabtarwa an tura su don hukumomin aka aikewa rahoton aikata laifukan su yi la'akari da su; sannan
- Iya tura kwafi-kwafi na bayanan ilmi na musamman na yaron da bayanan ladabtarwa kawai da Dokar Hakkokin da Sirrin Ilmin Iyali (**FERPA**) ta bayar da izinin.

## Sirranta Bayanai

Kamar yadda aka yi amfani a wannan sashe:

**Ruguzawa** na nufin ruguzawa ta zahiri ko cire abubuwan gane mutum daga bayanai ta haka ba za a iya sake gane bayanan ba.

**Bayanan Ilmi** na nufin nau'in adanannun bayanai da suka shiga cikin *bayanan ilmi* kamar yadda aka bayyana a cikin in 34 CFR Part 99 (dokokin da ke aiwatar da Dokar Haƙƙokin da Sirrin Ilmin Iyali (FERPA) ta 1974, 20 U.S.C. 1232g).

**Hukumar Shiga** na nufin kowace gundumar makaranta, hukuma, ko cibiya da ke tattara, kiyaye, ko amfani da bayanan gane mutum, ko daga bayanan da aka samu a ƙarƙashin IDEA Sashe na B.

**Bayanin mutum da ake iya ganewa** ya haɗa da: sunan yaronka, sunanka a matsayin mahaifi, ko sunan wani daga cikin iyali; adireshin yaronka; wata hanyar gane mutum kamar Lambar Zama Ɗan Kasa; ko jerin halayen mutum ko wani bayani da zai iya sa a gane yaronka kuma da cikakken tabbaci.

Kana da haƙƙin yin bitar dukan bayanan ilmi da aka ajiye na yaronka da suka ƙunshi ɓangarorin da suka shafi ilmi na musamman. Makaranta za ta dauka cewa kana da ikon saka ido da yin bitar bayanan da aka ajiye na yaronka sai fa idan an bayar da shawarar cewa ba ka da wannan iko a bisa dokar jaha da ta shafi irin waɗannan lamurran kamar reno, rabuwa, da kuma saki na aure. Kana kuma iya ba wani izinin ya yi bayanan da aka ajiye na yaronka. Idan ka nemi a yi bitar bayanan da aka ajiyen, to dole ne makaranta ta samar da su cikin hanzari kafin gudanar da taron da ya shafi IEP na yaronka, kafin kowane shirin sauraren bahasi ko zaman sulhu, sannan ko ta yaya kada ya zarce kwana 45 na kalanda daga lokacin da aka buƙaci hakan.

**Shaida, Kwafi-kwafi, Kuɗi**

Idan ka tambaya, dole ne makarantar ta yi maka bayani sannan ta fassara bayanan da aka ajiye, a bisa hujja. Dole ne makaranta ta samar da kwafi-kwafi idan wannan kawai ce hanyar da za ka iya samun damar saka ido da yin bitar bayanan da aka ajiyen. Mai yiwuwa makarantar ba za ta caje ka kuɗi ba don gudanar da bincike ko gano kowane bayanin ilmi daka ajiye game da yaronka. Haka kuma, ya yuwu ta caje ka kuɗin yin kwafi idan biyan kuɗin ba zai hana ka gudanar da saka idon da bitar bayanan da aka ajiyen ba.

**Bayanan akan Yaro Fiye da Ɗaya**

Idan kowane bayanin ilmi da aka ajiye wanda ya fi na yaro ɗaya, kana da haƙƙin saka ido da bitar bayanin da ke da alaƙa da yaronka kawai ko kuma a sanar da kai wannan takamaiman labarin.

Kana da haƙƙin nema da samun jerin nau'i da wuraren da aka tattara bayanan ilmin da aka ajiye, kiyaye, ko makaranta ta yi amfani da su.

**Amincewa da Bayyana Bayanan Gane Mutum**

Har fa sai idan akwai bayanan cikin bayanan ilmi da aka ajiye, sannan aka yarda da bayyana su ba tare amincewar iyaye ba a ƙarƙashin FERPA, dole ne a samu amincewarka kafin a bayyanawa wasu na daban bayanan gane mutum in dai ba jami'an hukumomin da ke halarta ba ne. Ba a neman amincewarka kafin a

sakarwa jami'an hukumomin da ke halarta bayanan gane mutum bisa dalilan cimma buƙatar shirin IDEA Sashe na B.

Amincewarka, ko amincewar yaron da ya cancanta ya kuma kai shekarun hankali na mafi yawa a ƙarƙashin dokar jaha, dole ne a samu bayanan gane mutum kafin a saki bayanan ga jami'an hukumomin da ke halarta da ke samar da ko biyan ayyukan miƙawar.

Idan an saka yaronka makaranta, ko ake shirin saka shi, a makaranta mai zaman kanta da ba wuri guda ta ke da makarantar gundumar da kake zaune ba, dole ne a samu amincewarka kafin a sakarwa jami'an hukumomin da ke halarta bayanan gane mutum game da yaronka tsakanin jami'an makarantar gunduma in da makarantar mai zaman kanta ta ke da jami'an makarantar gundumar da kake zaune.

Dole ne makarantar ta ajiye littafi don kowa, in ban da kai da jami'an makaranta da aka amince da su, da kan yi bitar bayanan da aka ajiye na ilmi game da yaronka, sai fa idan ka amince da a bayyana su. Wannan littafi dole ya ƙunshi sunan mutum, ranar da aka bayar da amincewa, da dalilin da aka ba mutumin don yin amfani da bayanan da aka ajiye.

Dole ne jami'i guuda daga makaranta ya dauki alhakin tabbatar da kiyaye sirrin kowane bayanin gane mutum. Dukan mutanen da ke tattara, ko amfani da bayanan gane mutum to dole ne su samu horo ko sanin ƙa'idoji dangane da manufofin jahar da hanyoyin da suka shafi kiyaye sirri a ƙarƙashin shirin IDEA and FERPA. Dole ne kowace makaranta ta kiyaye, don ziyarar mutane, sabbin jerin sunaye da matsayi na wadannan ma'aikatan cikin makaranta da za su iya samun bayanan gane mutum.

**Gyaran Bayanan da aka Ajiye**

Idan ba yarda cewa bayanin da aka ajiye na ilmin yaronkaba daidai yake ba, ya kauce, ko danne haƙƙoƙin yaronka, kana iya neman makaranta ta gyara bayanin. A cikin ƙayyadadden lokaci, dole ne makaranta ta yanke shawarar ko zai yuwu ta gyara bayanan. Idan makarantaar ta ƙi gyara bayanan kamar yadda aka nema, to dole ne ta sanar da kai kan ƙin amincewar da haƙƙinka na saurare don ƙalubalantar bayanan da aka ajiyen. Wannan nau'in sauraren yana cikin tsarin sauraren bahasi na cikin gida a ƙarƙashin tsarin FERPA sannan ba irin tsarin sauraren bahasi na IDEA ba ne da akan gudanar a gaban wani jami'i saurare ba.

Idan, sakamakon sauraren, makarantar ta yanke shawarar cewa bayanan ba daidai suke ba, sun kauce, ko kuma karya sirri ko danne haƙƙoƙin yaronka, dole ne a canza shi a kuma sanar da kai a rubuce. Idan, sakamakon sauraren, makaratnatar ta yanke shawarar cewa bayanan ba daida suke ba, sun kauce, ko karya sirri ko danne haƙƙoƙi na yaronka, to dole ne a sanar da kai na samun damar yin bayani a kan bayanin da ke cikin bayanan da aka ajiye na yaronka muddin bayanan da aka ajiye ko wani sashin da ake jayayya suna hannun kulawar makarantar.

Idan ka janyye amincewarka a rubuce game da samun ilmi na musamman ga yaronka da ayyuka masu alaƙa bayan da makaranta ta samarwa yaronka ayyukan tun da farko, to ba za a buƙaci makaranta ta gyara bayanin da aka ajiye na ilmin yaronka don cire kowane abu ga yaronka ya samu ilmi na musannan da ayuka masu alaƙa a baya. Haka kuma, har yanzu kana da haƙƙin neman makaranta ta gyara bayanin da aka ajiye na yaronka idan har ka yarda bayanan ba daida suke ba, sun kauce, ko danne haƙƙoƙin yaronka.

**Kariya da Rugazawa**

Dole ne makarantar ta bayar da kariya kan kiyaye sirrin bayanan da aka ajiye na yaronka, tattara, adana, bayyana, da matakan ruguzawa. Ruguzawa na nufin ruguzawa ta zahiri ko cire abubuwan gane mutum daga bayanai ta haka ba za a iya sake gane bayanan ba. Dole makarantar ta sanar da kai sa'adda ba a buƙatar bayanan da aka ajiyye na yaronka don samar da ayyukan ilmi ga yaron naka. Dole a lalata bayanan bisa buƙatark sai dai ban da suna, adireshi, lambar waya, maki, bayanan zuwa hallara da aka ajiye, azuzuwan da aka halarta, darajar maki da aka kammala da shi, da shekarar da aka kammala.

**Sanarwa ga Iyaye**

TEA zai bayar da sanarwa da za ta wadatar sanar da kai cikin sirri akan bayanan gane mutum, da suka ƙunshi bayanin tsawon yadda sanarwar da akan bayar za ta kasance cikin harshen gida na rukunin mutanen jahar; bayanin yaran da za kiyaye bayanansu na gane mutum, nau'in bayanan da ake nema, hanyoyin da a kan yi amfani da su wajen tattara bayanan, ciiki har da sassan da aka samo bayanan, da amfanin da aka samu daga bayanan; dole ne a saka takaitattun manufofi da tsare-tsaren hukumomin da suka shiga dangane da adanawa, bayyanawa ga wasu na daban, riƙewa, da lalata bayanan da ake gane mutum; da bayanin dukan haƙƙokin iyaye da yara dangane da waɗannan bayanai, ciki har da haƙƙin da ke ƙarƙashin ikon FERPA da ƙa'idojin da ta ke aiwatarwa a cikin 34 CFR Sashe 99.

## Gurabun Sa Kai Na Makaranta Mai Zaman Kanta Na Iyaye

Kana da takamaiman haƙƙoki yayin da ka saka yaronka makaranta mai zaman kanta bisa raɗin kanka. IDEA baya buƙatar makarantar gwamnati ta b iya kudin ilmi, ciki har da ilmi na musmamman da ayuka masu alaƙa, ga yaronka mai fama da lalura a makaranta mai zaman kanta ko kayan aiki idan makarantar gwamnati ta samar da tsarin FAPE ga yaronka sannan ka zabi ka saka yaron a makaranta mai zaman kanta ko kayan aiki. Haka kuma, makarantar gwamnati in da makaranta mai zaman kanta ta ke dole ne ta saka yaronka cikin waɗanda ake magance buƙatarsu a ƙarƙashin tanada-tanaden tsarin IDEA da ya shafi yara da iyayensu suka saka a makaranta mai zaman kanta.

### Buƙata don Cike Gurbi Ɗaya na Iyayen Yaran da ke Makaranta Mai Zaman Kanta Makarantun da Jama'a ke Biya

Kana da takamaiman haƙƙin yayin da ka saka yaronka a makaranta mai zaman kanta saboda ba ka amincea da makarantar gwamnati ba dangane da rashin irin shirin da ya dace da yaronka.

Idan a baya yaronka ya taba samun ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa a ƙarƙashin ikon makarantar gwamnati sannan ka zabi ka saka yaronka a makaranta mai zaman kanta, makarantar firamare, makarantar sakandire ba tare da amimcewar ko sa hannun makarantar gwamnati, kotu ko wani jami'in mai auraren bahasi na iya buƙatar makaranta ta biyanka kudin da ka kashe wajen sakawar idan kotu ko jami'in sauraren ya samu cewa makarantar gwamnati ba ta samarwa yaronka tsarin FAPE ba a cikin lokaci kafin sakawar sannan cewa gurbin makaranta mai zaman kanta ya dace. Jami'i mai sauren bahasi ko kotu na iya samun cike gurbin naka ya zama wanda ya dace koda kuwa cike gurbin bai cimma cikakkun sharuddan da aka gindaya da suka shafi tsarin ilmi na TEA ya samar da makarantu.

### Iyankacewa kan Biya

Yawan kuɗin da aka bayyana a cikin sakin layin da ke biye na iya raguwa ko ƙi idan: taron kwamitin ARD da ka halarta kwanan nan kafin ka cire yaronka daga makarantar gwamnati, ba ka sanar da kwamitin ARD ba cewa ka ƙi karbar gurbin da makarantar gwamnatin ta samar maka na FAPE ga yaronka, ciki har da bayyana damuwarka da manufarka ta saka yaronka makaranta mai zaman kanta da kuɗin jama'a; ko akalla kwanakin aiki 10, ciki har da kwanakin hutu da suka shigo cikin kwanakin aiki, kafin cire yaronka daga makarantar gwamnati, ba ka ba makarantar gwamnati sanarwar bayanin a rubuce ba; ko, kafin cirewar da ka yi wa yaronka daga makarantar gwamnati, makarantar gwamnati ta samar maka da sanarwa a rubuce tun da farko na shirinta na tantance yaronka, ciki har da bayanin dalilin gudanar da tantancewar da ta dace kuma akan dalili, amma ba ka gabatar da yaron wajen tantancewar ba; ko kotu ta samu cewa matakin da ka ɗauka bai bisa ƙwƙƙwaran dalili.

Haka kuma, dole ba za a rage kuɗin ba ko hana su don kasa samar da sanarwar idan: makarantar gwamnati ta hana ka samar da sanarwar; ba ka samu sanarwar ba na alhakin da ke kanka na samar da sanarwar da aka bayyana; ko yin daidai da buƙatun da ke tafe na iya cutar da yarnka a zahiri. A bisa hukuncin kotu ko jami'in

sauraren bahasi, yawan kudin da za a biya ka na iya raguwa ko a hana don kasawarka wajen samar da gamsasshiyar sanarwa da aka buƙata idan har ba ka da ilmi ko ba ka iya rubutu a harshen Ingilishi ba, ko yin daidai da buƙatun da ke tafe na iya haifar da babbar damuwa gga yaronka.

## Miƙa Haƙƙoƙin Iyaye

Dukan haƙƙoƙin iyaye a cikin tsarin IDEA a kan miƙa su ga yaro yayin da yaron ya kai shekarun mafi yawa. Shekarun mafi yawa a ƙarƙashin dokar Texas su ne shekara 18. Ga mafi yawan yara, dukan haƙƙoƙin iyaye da aka tattauna a wannan kundi za saka su a yaron da ya kai aƙalla shekara 18. Yayin tura haƙƙoƙin iyaye zuwa ga ɗalibi babba,, shi ko ita na da damar yanke hukunci akan ilmi, duk da ya ke dole ne makarantar gwamnati ta samar maka da sanarwar taron kwamitin ARD da sanarwoyi a rubuce. Kai, haka kuma, kana iya ƙin halartar tarukan har sai babban ɗalibi ya gayyace ka ko makaranta ko sai babban ɗalibinka ya ba ka wannan damar a bisa matakin da aka goyi baya ta hanyar-yarjejeniya.

### Mai Reno da Kotu ta Naɗa don Babban Ɗalibi

Idan har kotu ta naɗa ka ko wani mutum a matsayin mai kulawa da ɗalibi a bisa doka, to ba za miƙa haƙƙoƙin da ke ƙarƙashin IDEA zuwa ga babban ɗaliibi. Wanda aka naɗan bisa tsarin shari'a zai samu haƙƙoƙin.

### Babban Ɗalibi da aka Ɗaure

Idan an ɗaure babban ɗalibi, to dukan haƙƙoƙin IDEA za a miƙa su ne ga babban ɗalibin da ya kai shekara 18. Ba za ka ci gaba da samun damar sanarwa a rubuce da ta shafi ilmi na musamman ba.

### Ɗalibai Manyan kafin Shekara 18

Akwai wasu sharuɗɗa da aka bayyana a Babi na 31 na Dokar Iyali a Texas da ta shafi yaron da ke girma kafin ya cika shekara 18. Idan aka kuduri yanke hukunci a cikin wannan babi cewa yaronka babba ne, to nan take za a miƙa wa yaron haƙƙoƙin da ke ƙarƙashin shirin IDEA.

### Zaɓin Tsarin Kulawa

Dole ne makarantar gwamnati ta karrama ikon wakili mai inganci ko matakin goyon bayan-yarjejeniya mai inganci da babban ɗalibinka ya aiwatar.

### Sanarwoyi da Bayanai da ake Buƙata

A ranar ko kafin ranar cikar yaro shekara 17, dole ne makarantar gwamnati ta samar maka da kuma yaronka sanarwa a rubuce tana bayyana miƙa haƙƙoƙin mahaifi zuwa ga yaro ciki har da bayani game da kula da zabin kulawa, ciki har da matakin-yarjejeniya da aka goya ma baya, da sauran goyon baya da ayyuka da za su iya taimakon yaronka ya dogara da kan sa. Dole ne IEP na yaronka ya bayyana cewa makarantar gwamnati ce ta samar da wannan bayanin.

A ranar cikar yaronka shekara 18, dole ne makarantar gwamnati ta samar maka da yaronka sanarwa a rubuce cewa za a miƙa haƙƙoƙin iyaye zuwa ga babban ɗalibi. Dole ne wannan rubutacciyar sanarwa ta ƙunshi bayanan da sassa game da kulawa da zabin zuwa ga kulawar, ciki har da bayani game da kula da zabin kulawa, ciki har da matakin-yarjejeniya da aka goya ma baya, da sauran goyon baya da ayyuka da za su iya taimakon yaronka ya dogara da kan sa. Kuma dole ne wannan rubutacciyar sanarwa ta ƙumnhi bayanan tuntuɓa da za a yi amfani da wajen neman ƙarin bayani.

## Bayanan Ilmi Na Musamman

Idan kana buƙatar bayani game da lamurran ilmi na musamman, kana iya kiran Cibiyar Bayanan Ilmi Na Musamman a 1-855-SPEDTEX (1-855-773-3839). Idan ka kira wannan lamba ka bar saƙo, wani zai kira ka ranakun aiki. Mutanen da suke kurame ne ko masu lalura ji na iya kiran lambar SPEDTEX ta amfani da Relay Texas 7-1-1.

## Sulhunta Ɓaraka

Akwai lokutan da kana iya samun rashin jituwa da matakan da makarantar da ke ba yaronka ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa ta ɗauka. Kana da

ƙwarin guiwar yin aiki tare da jami'in makaranta don samar da daidaito. Kana iya tambayar makaranta game da wane irin tsarin sulhu shirin kan ba iyaye. Tsarin TEA kan samar da zabi huɗu don samar da sulhu ga jayayya da ta shafi ilmi na musamman: tsarin IEP na sauƙaƙawa na jahar, ayyukan shiga tsakani, shirin samar da sulhu, da shirin sauraren bahasi.

### Bambanci tsakanin Tsare tsaren Koken da Saurare da Koken akan Ilmi na Musamman

Dokokin Ilmi na musamman na Tarayya sun fito da wasu tsare-tsare kan amsa koke da ya shafi ilmi na musamman da koken saurare da kuma sauraren bahasi. Kamar yadda aka bayyana a sama, kowane mutum ko hukuma, ciki har da guda a cikin jaha, na iya shigar da wani koke na musamman yana zargin karya sharuddan doka ta kowace IDEA Sashe na B, ko kuma kowace hukuma ta jama'a. Kai ko makaranta kaɗai ke iya shigar da koke kan kowane lamari da ya shafi nufi ko kin soma ko canza abubuwan ganewa, tantancewa, gurbin karatu na yaro mai fama da lalura, lo tanadin da FPE ya yi ma yaron. Yayin da dole gadaɗaya tsarin TEA ya sasanta koke akan ilmi na musamman cikin kwanakin kalanda 60 na jadawalim lokaci, sai fa idan an ƙara lokacin a bisa tsari, to dole ne wani jam'in sauraren bahasi ya saurari koken (idan ba a sasanta shi ba ta hanyar taron sulhu ko shiga tsakani) a samar da mataki a rubuce cikin kwanakin kalanda 45 bayan lokacin sulhu ya ƙare, kamar yadda aka bayyana a cikin wannan kundi a ƙarƙashin taken Shirin Sulhu, sai fa idan jami'i mai sauraren bahasi ya bayar da damar ƙara tsawon jadawalin lokaci kamar yadda ka nema ko makaranta ta buƙata.

## Gudanar Da Tsarin IEP Na Jaha

Kamar yadda dokar jaha ta nema, TEA ne ya samar da masu gudanar IEP mai zaman kansa don taimakawa kwamitin ARD gudanar da zama don sassan da ke jayayya mgame da matakai da suka danganci tanadin da FAPE ya yi yaro mai fama da lalura. Sharuddan da suka zama dole su yi daidai da TEA don samar da masu gudanarwa masu zaman kansu su ne kamar haka:

- Dole ne a cike takardar buƙata da sa hannunka da na makaranta. Ana samun wannan takardar cikewa a cikin Ingilishi da Sipaniyanci, a yanar gizo a [Shirin Gudanar Da Ilmi Din Al'umma (Kafa: bit.ly/3spluIV).](bit.ly/3spluIV) Ana kuma iya samun sa idan an nema daga TEA.
- Dole ne jayayyar ta shafi taron kwamitin ARD a samu yarda tsakanin juna game da abu ɗaya ko fiye na abubuwan da tsarin IEP bai kai gare su ba sannan kwamitin ARD ya yarda ya ci gaba kuma ya kira taron.
- Dole ne TEA ta nemi takardar cikewar cikin kwanakin kalanda goma na taron kwamitin ARD da ba a cimma matsaya ba, sannan dole ne mai gudanarwa ya zo a lokacin da za a kara sake kiran taro.
- Dole ne kai da makaranta ku shiga cikin tsarin gudanarwa na IEP da ya shafi yaron da ke cikin wannan makarantar a wannan shekarar karatu na saka wannan buƙatar don gudanar da IEP.
- Ana iya samu tsarin Jaha mai alaƙa da shirin gudanarwar IEP na jaha a [19 TAC §89.1197 (Kafa: bit.ly/3bCULCL).](bit.ly/3bCULCL)

## Ayyukan Shiga Tsakani

Dole ne a samar da tsarin shiga tsakani don magance jayayyar da ta shafi kowane irin lamari a ƙarƙashin tsarin IDEA Sashe na B, ciki har da lamurran da ke tasowa kafin shigar da koke akan sauraren bahasi. Ta haka, an samar da tsarin shiga tsakani don magance jayayya a ƙarƙashin tsarin IDEA Sashe na B, ko da kuwa ka saka koken neman sauraren bahasi kamar yadda aka bayyana a ƙarƙashin taken Tsare-tsare Masu Kyau. Ba taƙaiice shiga tsakani kan jayayya tsakanin iyaye da makarantu ba dangane da ganowa, tantancewa, ko samar wa ɗalibi da gurbin karatu, ko tanadin FAPE ga yaron.

Shiga tsakanin na ƙashin kai ne. Ta haka, idan ku biyu kai da makarantar kuka shiga tsakanin na ƙashin kanku, TEA kan tsara ya kuma biya kan shiga tsakanin. Ba mai yuwa ne a yi amfani da shiga tsakanin don jinkirta ko hana samun sauraren bahasi ko wasu haƙƙoƙi a ƙarƙashin tsarin IDEA.

Kai tsaye TEA kan samar da shirin shiga tsakani a kowane lokaci aka nemi yin sauraren bahasi. Amma, kana iya neman ayyukan shiga tsakanin kowane lokacii ka da makaranta kuka kasa cimma yarjejeniya game da kowane lamari a ƙarƙashin tsarin IDEA Sashe na B.

Masu shiga tsakani ba ma'aikatan TEA ba ne ko gundumar makarantar da ta shiga cikin tsarin ilmi ko kula da yaro da shirin shiga tsakanin ya sahafa, sannan ba za su iya sa ra'ayinsu ko na wani ra'ayin aiki da zai iya kawo cikas ga ƙudurinsu ba. Duk wanda ta wata hanya ya cancanci zama mai shiga tsakani ba ma'aikacin makarantar gunduma ko TEA ba ne saboda ko TEA na biyan sa ko biyan ta don yin aiki a matsayin mai shiga tsakani. Masu shiga tsakani ƙwararru ne da suka cancanta da kuma samun horo kan samar da sulhu da kuma su ke da ilmin shari'a na musamman. Aikin mai shiga tsakani shi ne cimma ƙuduri sannan a yayin shiga tsakanin kada ya karkata wani sashe guda na kowa a. Burin da ake son cimma wajen shiga tsakani shi ne a taimaki kai da makaranta cimma yarjejeniyar da za ta yi muku daidai.

Ana iya samun kafar da masu shiga tsakani na yanzu a [Babban Ofishin Bayar Da Shawara, Shirin Shiga Tsakani Na Musamman (Kafa: bit.ly/39yQTjK).](bit.ly/39yQTjK)

Idan kai da makaranta kuka amince da a shiga tsakani, kuna iya yarda ku yi amfani mai shiga tsakanin na musamman, ko mai shiga tsakanin da aka zaɓa kawai. A kowane dai, mai shiga tsakanin zai tuntuɓe ku cikin lokacin da aka tsara zaman shiga tsakanin a wuri da lokacin da ya yi ma kai da makaranta daidai.

Dole ne a sirranta tattaunawar da za ta auku a lokacin shiga tsakanin. Ba za a iya amfani da su a matsayin hujja a shirin sauraren bahasi na gaba ko zaman kowace kotun tarayya ko jaha da kan samu tallafin IDEA Sashe na B.

Idan kai da makaranta kun magance matsalar ta hanyar shirin shiga tsakani, to kowane bangaren biyu zai yi yarjejeniya a shari'ance cewa zai ci gaba da martaba sulhun nan gaba. Dole ne yarjejeniyar ta bayyana cewa dukan tattaunawar da aka yi lokacin shiga tsakanin ta zama a sirrance sannan ba za yi amfani da ita a matsayin hujja a wani sauraren bahasi na gaba ba ko sauraren ƙara. Dole ne kai da wakilin gundumar makaranta mai ikon yanke hukunci kan makarantar ku saka hannu a yarjejeniyar. Rubutacciyar, yarjejeniyar da aka sanyawa hannu ta zama doka kuma sannan zartacciya a kowace kotu mai iko ƙarƙashin dokar jaha don sauraren wannan shari'a ko a kotun gunduma ta tarayya.

Kana iya samun samun ƙarin bayani game da shirin shiga tsakani a shafin yanar gizo na TEA a [Babban Ofishin Bayar Da Shawara, Shirin Shiga Tsakani Na Musamman (Kafa: bit.ly/39yQTjK).](bit.ly/39yQTjK)

A na iya samun hukuncin jaha mai alaƙa da shirin shiga tsakanin na ilmi na musamman [19 TAC §89.1193 (Kafa: bit.ly/35Dyrp2).](bit.ly/35Dyrp2)

## Shirin Shigar Da Koke Na Ilmi Na Musamman

Wani zabin samar da sulhu akan jayayyar da ta shafi ilmi na musamman shiri ne na shigar da koke na ilmi na musamman na TEA. A wannan kundi, ma'anar koke akan ilmi na musamman na nufin koke matakin jaha ƙarƙashin IDEA da aiwatar da dokokinta. Idan ka yarda wata hukumar jama'a ta sabawa sharuddan ilmi na musamman, ko idan ka yarda cewa wata hukumar jama'a ba ta aiwatar da matakin sauraren bahasi, kana iya aika koke a rubuce zuwa ga TEA. Dole ne ka aika da kokenka zuwa ga wanda aka yi koke saboda shi a lokaci guda kuma ka aika da koken zuwa ga TEA. Kowace hukuma ko wani mutum, ciki har da ɗaya daga wata jaha, na iya shigar da koke kan ilmi na musamman tare da TEA. Lokacin da aka sakawa koken zai soma a cikin kwanakin aiki na gaba daga ranar da TEA ya samu ƙorafinka.

TEA ya samar da wata takardar cikewa don tallafawa iyaye da wasu na daban shigar da koke dangane da ilmi na musamman. Bangaren da ya shigar da koke game da sha'anin ilmi na musamman na iya amfani da tsarin

takardar cikewar ta jaha ko wani kundi muddin koke ya ƙunshi dukan bayanan da aka buƙata.

Dole ne rubutaccen kokenka ya bayyana laifin da ya faru cikin abinda bai zarce shekara guda ba kafin ranar da aka samu koken. Dole ne koken ya ƙunshi: bayanin da ya nuna hukumar lura da jama'a ta ya aikata laifin da ya shafi sharuɗɗan ilmi na musamman, hujjar da aka kafa bayanan da ita, da sa hannunka da bayanan tuntuɓa. Idan koken ya shafi takamaiman yaro, to dole ne koken ya ƙunshi: sunan yaro da adireshinsa ko wani bayanin tuntuɓa idan har yaron ba shi da gidan zama, sunan makarantar yaron, da bayanin yanayin matsalar yaron, ciki har da haƙiƙanin abinda ya haddasa matsalar gwargwadon sani sannan kake da su a lokacin. Dole ne koken ya kunshi shirin samar da sulhu kan matsalar gwargwadon sanin lamarin sannan ake da su a lokacin da aka shigar da koken.

Da zaran an samu koke kan ilimi na musamman, hukumar TEA za ta ba mai shigar da koke damar miƙa ƙarin bayani dangane da zarge-zargen da ke cikin koken, ko da baki ko a rubuce. Haka kuma hukumar TEA zai ba Hukumar Lura Da Jama'a damar bin kadin koken da kuma bata damar miƙa shawarar magance matsalar da aka yi koken. Kuma, Hukumar TEA zai ba mahaifin da ya shigar da ƙorafin da Hukumar Lura Da Jama'a damar hawan teburin sasanci.

Cikin kwanakin kalanda 60 bayan samun koke game da sha'anin ilmi na musamman, TEA zai gudanar da bincike, ciki har da binciken wuri idan ya zama dole. Kwanaki 60 na kalanda na jadawalin lokacin da aka shata don sulhunta koken ana iya ƙara shi saboda wasu dalilai da suka faru masu nasaba da wani koke daban duk sassan biyu game da koke akan ilmi na musamman su yarda da ƙarin don gudanar da shiga tsakanin ko bin wasu hanyoyi na daban na sulhunta jayayyar.

A gudanar da binciken, TEA zai yi bitar bayanai masu alaka su yi wani ƙuduri mai zaman kansa akan ko hukumar lura da jama'a ce ta karya dokar tarayya ko ƙa'adojin ilmi na musamman na jaha. TEA za ta samar da mataki a rubuce ta na mai magance kowadanne zarge-zarge ciki kuwa har da gano gaskiya, kammalawa, da dalilan matakin TEA.

Wajen magance wani ƙorafi da aka shigar da TEA ya gano akwai kasawa wajen samar da ayyukan da suka dace, dole ne TEA ya magance matsalar kasawar samar da ayyukan da suka dace tukun, da suka ƙunshi matakan da suke daidai da suka dace wajen biyan wasu buƙatun yaron (kamar hidimomin biyan diyya ko biyan kuɗi) da tanadin da ya dace na wasu hidimomi ga yara masu fama da lalura.

Matakin TEA da ya shafi koke akan ilmi na musamman shi ne ta ƙarshe kuma ba za ɗaukaka ƙara ba.

Shigar da koke ba ya janye hakkinka na neman shiga tsakani ko neman sauraren bahasi. Idan ka shigar da koke ka kuma nemi a gudanar da sauraren bahasi game lamari guda, TEA zai janye kowane lamari a cikin koken da ake cikin magance matsalarsa a sauraren ba'asi har sai an kammala sauraren. Kowace irin matsala a cikin koken da ba ya cikin lamarin sauraren bahasi za a a magance ta cikin lokacin da da kuma tsara sannan tsare-tsaren da aka bayyana a cikin wannan kundi.

Ida aka yanke shawarar kan maganar wata matsala a koken da ake son yin sauraren bahasi ya ya kumshi sassa iri daya, matakin ya shiga cikin lamarin, sannan TEA zai sanar hakan nan take.

Dole ne TEA ya samar da rubutattun tsare-tsare don raba tsare-tsarensa kan koken zuwa ga iyaye da sauran masu sha'awa, ciki kuwa har da horas da iyaye da cibiyoyin tara bayanai, hukumomin kwatanta gaskiya da samar da kariya, cibiyoyi masu zaman kansu, da wasu abubuwan da suka dace.

Dole ne TEA ya zama yana da tsare-tsare a rubuce don tabbatar da kyakkyawar aiwatar da matakinsa na karshe, idan akwai buƙata, ciki har da: (a) ayyukan taimako na fasa; (b) tattaunawa; da (c) sahihan matakai don cimma daidaito.

Kana iya samun ƙarin bayani game da koke akan ilmi na musamman da takardar cikewa ta koke a shafin yanar gizo na TEA a [Shirin Samar da Sulhu Kan Jayayya akan Ilmi na Musamman (Kafa: bit.ly/3bL6n73).]()

A na iya samun hukuncin jaha mai alaƙa da shirin shiga tsakanin na ilmi na musamman [19 TAC §89.1195 (Kafa: bit.ly/35IU1rY).]()

## Kyakkyawan Shiri Tsare-tsare

Zaɓi na huɗu don magance matsala kan jayayya da ta shafi ilmi na musamman shiri ne na sauraren bahasi. A yayin sauraren bahasi, jami'in sauraren da ba ya karkata kan saurari hujjoji daga sassan sannan ya yanke hukunci a dokance.

Dole ne a shigar da ƙorafin cikin shekaru biyu na watan da ka sani ko ya kamata ka sani game da matakin zargin da ya haifar da dalilin yin ƙorafin. Wannan tsarin lokaci ya zama ƙ'idar da aka iyakance. Wannan jaddawali bai yi daidai da kai ba idan an hana ka shigar da koke kan ƙa'ida saboda bayanan da ba daidai ba daga makaranta cewa ta riga ta magance matsalar ko saboda makaranta ta riƙe wani bayani ta hana ma ka da kuma ake buƙatar a ce an samar maka da shi. Yayin da ba buƙatar IDEA ce ba, jahar Texas ta samar da cewa a wasu lokuta , ka'idar da aka iyakance ta shekara biyu don shigar da koke ana iya bayar da ita ko tsayar da ita idan kai ma'akaci ne ko soja, Jami'i a Hukumar Lura Da Yanayi Da Teku Ta Kasa ko Hukumar Jami'an Tsaro ta Lafiya ta Amurka, sannan a ƙa'idar da aka iyakance tanadin da dokar tarayya da aka sani da suna Dokar Samar Da Sassauci Ga Ma'aikata zuwa gare ka.

Idan ka shigar da koke don neman a yi sauraren bahasi, kana da wani nauyi ne na tabbatar da cewa makaranta ta aikata laifi game da lamarin ilmin na musamman da ake buƙata. A wasu lokuta, makaranta na iya shigar da koke tana neman a gudanar da sauraren bahasi a kan ka. A wadannan lokutan, makaranta na dauke da nauyin samar da hujja.

Kafin ka yi ƙarar makarantar a gaban kotu game da kowane lamari da aka lissafo a baya, dole ne sai ka shigar da koke tukun. Idan kuma ba ka yi haka ba, kotu na iya watsi da ƙarar da ka shigar.

### Neman Gudanar da Saurare

Kai ko makaranta na iya rasa shigar da koke har sai kai ko makaranta (ko lauyanka/wakili ko lauyan makaranta/wakili) ya shigar da koken da ya hada da: sunan yaronka da adireshi ko bayanan tuntuba idan yaron ba shi da gidan zama; sunan makarantar yaronka; bayanin matsalar da yaronka ke fama da ita, ciki har da gaskiya dangane da matsalar da ka shiga gwargwadon yadda ka sani kuma ka same ta a lokacin.

Ana samun takardar cikewa ta shigar da koke daga TEA a [Babban Ofishin Bayar Da Shawara, Shirin Shiga Tsakani Na Musamman (Kafa: bit.ly/2XCdKFw).]()

Ba dole ne sai ka yi amfani da takardar cikewa ta TEA ba, amma dole ne kokenka ya ƙunshi bayanan da ke sama.

Kai, lauyanka, ko wakilinka (ko makaranta, lauyanta, ko wakilinta) dole ne su aike da koken a rubuce zuwa ga TEA sannan a lokaci guda da ɓangaren da suke jayayya. Dole a sirranta koken.

Don a tura koken zuwa gaba, dole ne ya samu cikakken yi la'akari (ya dace da sharuɗɗan da ke sama). Koken da ke kan ka'ida za a yi la'akari da shi sosai sai fa idan wani na daban da ke samun koken (kai ko makarantar) kan sanar da jami'in sauraren bahasi da wasu na daban a rubuce cikin kwana 15 na kalanda da samun koken, cewa wani na daban da ya samu koken ya yarda cewa shirin sauraren bai cika sharuɗɗan da aka lissafo a sama ba.

A cikin kwana goma na kalanda da samun sanarwar cewa wani na daban mai samun koken (kai ko gundumar makaranta) kan yi la'akari da koken a matsayin wanda bai gamsar ba, dole jami'in sauraren bahasi ya yanke shawarar idan tsarin koken da aka shigar ya cika sharuɗɗan da aka ambata a sama sannan ya sanar da kai da makaranta a rubuce da hanzari.

## Amsar Gundumar Makaranta akan Shigar da Koke

Idan har makaranta ba ta riga ta tura maka sanarwa a rubuce ba a ƙarƙashin kundi na 34 CFR §300.503 dangane da batun da ke cikin koken, dole ne ta aika maka da nata ba'asin cikin kwana 10 daga sadda ta samu kokenta wanda shi ba'asin zai ƙunshi:

- Bayanin dalilin da ya sa ka nufi ko fasa daukar matakin da aka tado a lokacin shigarwa;
- Bayani dalla-dalla na wasu zabi da kwamitin ARD ya yi la'akari da su da dalilan da ya sa aka yi watsi da waɗannan zabin;
- Bayani dalla-dalla na kowace hanyar kimantawa, tantancewa, adana, ko rahoton da makaranta ta yi amfani da shi a matsayin hujjar shawarar ko ƙin ɗaukar mataki; da
- Bayani dalla-dalla na wasu abubuwa da ke da alaƙa da shawarar makarantar ko watsi da ita.

Samar da wannan bayani ba ya hana makaranta wajen tabbatar da cewa shirin shigar da koken bai wadatar ba, bai dace ba.

## Amsar Wasu Na Daban Ga Shigar Da Koke

Sai fa idan an bayyana a sashen da ke sama, wani da ke samun koke dole, cikin kwana 10 na kalanda da samun koke, ya aika ma wani na daban amsa cewa ya magance matsalar da aka shigar da koke kan ta.

Mahaifi ko makaranta na iya gyara ko sauya tsarin saka koke kawai idan wani na daban ya amince da canje-canjen a rubuce sannan a ka ba shi damar magance shirin shigar da koken ta hanyar taron sulhu ko idan jami'i mai saurare ya bayar da izini cikin abinda bai gaza kwana biyar ba na kalanda kafin a soma sauraren. Wanda ya nemi a yi sauraen mai yuwa ba zai kawo wasu batutuwa a lokacin sauraren ba wadanda ba a maganarsu a cikin koken sai fa idan wani na daban ya amince cewa za a iya ƙara wasu batutuwa. Idan wani ya shigar da koken, ko dai kai ko makaranta, kun gyara, (canza) tsarin shigar da koken jadawalin lokacin sulhu da jaddawalin lokacin da za a sake saurare ranar da aka shigar da koke kan gyaran da aka yi.

Dole ne ka samar da bayanai game da kowace shari'a ta kyauta ko mai saukin-farashi da ayyuka masu alaƙa a sashen da ka nemi bayanan ko idan kai ko makaranta kun shigar da koke.

## Matsayin Yaro lokacin Zama (Tsayawa)

In ban da zaman kotu da ya shafi ladabdatarwa, da zarar an aika da koke zuwa ga wani, a lokacin shirin sulhuntawar, da lokacin da ake jiran a yanke hukuncin sauraren bahasi da babu karkata ko zaman kotu, sai fa idan kai da jaha ko makaranta kun amince da wani abu daban, to dole ne yaronka ya ci gaba da zama a gurbinsa ko gurbinta na karatu. Ci gaba da zama a wuri na yanzu an fi sanin sa da tsayawa. Idan zaman ya shafi ladabtarwa, duba Cike Gurbi Lokacin Ɗaukaka Kara don tattaunawa game da cike gurbi na yaronka a lokacin ladabtarwa game da jayayya.

Idan koken ya haɗa takardar neman fara saka yaronka makarantar gwamnati, to dole ne a saka yaronka, idan ka amince, da shirin makarantar gwamnati har zuwa kammala dukan zaman. Idanonka na daf da cika shekara uku da sauyawa da ga shirin Lura Da Matakin Kurciya (ECI), tsayawa ba ta daga ayyukan ECI. Idan yaro ya cancanci samun ilmi na musamman da ayyuka masu alaƙa sannan iyayen sun amince, to dole a samar ayyukan da ba su cikin jayayyar.

Idan jami'in sauraren da ke cikin shirin shigar da koke da TEA ya gudanar ya amince dakai cewa ya dace ka sauya gurbin karatun yaronka, dole ne a lura da wannan sauyin wurin karatu kamar yadda aka cimma yarjejeniya tsakaninka da jaha. Haka kuma, wannan sauyin wurin karatu zai zama gurbin karatun yaronka na yanzu a lokacin jiran sakamakon ɗaukaka ƙarar.

## Kayyadadden Lokacin Sulhu

Sai fa idan a cikin shari'ar da ta shafi saurare, cikin kwanakin kalanda 15 na samun koken neman saurare, dole ne makaranta ta sake kiran taron da ake kira taron sulhu tare da kai, wakilin makaranta mai ikon yanke hukunci, da membobi masu dangantaka na kwamitin da ka zaɓo da kanka. A lokacin taron makaranta na iya

hadawa da wani lauya kawai idan kai ma kana da lauya a wurin gudanar da taron.

In dai ba kai da makaranta kuka riga kuka yarda a rubuce kun yafe shirin sulhun ko a maimakon haka sun yarda su amfani da tsarin shiga tsakani, to kuwa dole ne a gudanar da taron sulhun. Idan ba ku halarci taron sulhu ba, loakcin da aka shata na shirin sulhun da sauraen bahasi za a jinkirta shi har sai an gudanar da taron.

Idan makaranta ta yi wata himma don ganin ka halarci taron sulhun, amma ba ka halarta ba, sannan a karshen kwanakin kalanda 30 na ƙayyadadden lokacin sulhu, to makarantar na iya neman jami'in saurarre ya yi watsi da kokenka. Dole ne makaranta ta nuna wata himma don sa ka halarci taron ta bayanai kamar haka: bayanan da aka ajiye na makaranta ta yi ƙoƙarin tsarawa tsakaninkun da wuri da lokaci,, kamar bayanan kiran waya da aka yi ko aka yi niyyar yi da sakamakon wadannan kiraye-kirayen da aka yi ko niyyar yi da sakamakon waɗanna kiraye-kiraye; kwafi-kwafi na saƙon da aka tura maka da duk wata amsa da aka samu; da cikakkun bayanan ziyarar da aka yi zuwa gidanka ko wurin aikinka da sakamakon da ziyarar suka haifar.

Idan, a hannu guda, makaranta ta kasa gudanar da taron sulhu cikin kwanakin kalanda 15 da samun sanarwar game da koken da ka shigar ko kasa halartar taron sulhu, kana iya neman jami'in sauraren bahasi ya kawo ƙarshen ƙayyadadden lokacin sannan ya bayar da umurnin saka kwanakin kalanda 45 don soma saurare.

Yadda aka saba, wa'adin lokacin sulhu kan kai tsawon kwanakin kalanda 30. Haka kuma, idan kai ko makaranta kuka yarda a rubuce na yafe zaman sulhun, sannan lokacin kwanakin 45 na kalanda da aka saka don sauraren ya soma gobe. Haka kuma, idan kai da makaranta kun soma shirin shiga tsakani ko taron sulhu, amma kafin ƙarshen wa'adin sulhu cikin kwanaki 30 na kalanda, kai da makaranata kun yarda a rubuce cewa babu wata yarjejeniya mai yuwa, sannan lokacin kwanakin 45 na kalanda da aka saka don sauraren ya soma gobe. Daga ƙarshe, idan kai da makaranta kun yarda ku yi amfani da bayanan shirin shiga tsakani, to kowane bangaren biyu na iya yarda a rubuce don a ci gaba da shiga tsakanin a ƙarshen wa'adin kwanaki 30 na kalanda har a cimma yarjejeniya. Haka kuma, idan ko kai ko makaranta kuka yarda a rubuce na yafe zaman sulhun, sannan lokacin kwanakin 45 na kalanda da aka saka don sauraren ya soma gobe.

Idan sassan suka shigar da koken yin gyara a bisa ƙa'ida, lokacin da aka saka na gudanar da taron sulhu da wa'adin lokacin magance matsalar da ta shafi koken (wa'adin lokacin sulhu) sun dawo baya idan aka shigar da koken neman yin gyara.

Dalilan taron sulhu su ne don ba ka damar tattauna buƙatarka da muhimman batutuwa tare da makaranta sannan a ba makaranta damar magance matsalar jayayya wadda ta mamaye buƙatar. Idan kun cimma yarjejeniya a yayin taron, to dole kai da makaranta bayyana wannan yarjejeniya a rubuce sannan ku saka hannu. Wannan rubutacciyar yarjejeniya umurnin kotu ne wadda dokar jahar ta ba ta ikon sauraren irin wannan shari'a ko a kotun gunduma ta tarayya sai fa idan daya daga sassan ya kaucewa yarjejeniyar cikin kwanakin aiki uku daga ranar da aka sanya mata hannu.

Idan makaranta ba ta magance matsalar da ta taso ba a cikin koken da ka shigar ba daidai yadda ka so cikin kwanaki 30 na kalanda daga samun koken ka, loakcin saurare na kwanakin kalanda 45 kan somma sannan a iya soma sauraren.

### Wa'adin Lokacin Sulhu a Sauraren Gaggawa

Dangane da sauraren gaggawa, dole makaranta ta kira taron sulhu a cikin kawankin kalanda bakwai da samun koken neman sauraren bahasi. Kana da haƙƙin a gudanar maka da sauraren idan makaranta ba ta magance matsalar da aka taso da ita ba a cikin koken da ka shigar daidai yadda kake so cikin kwanaki 15 na kalanda da makaranata ta samu koken. Dole ne a gudanar da sauraren bahasin cikin kwanakin karatu 20 daga ranar da aka shigar da koken. Dole ne jami'in gudanar da sauraren ya bayyana da matakin ƙarshe cikin kwanakin karatu 10 bayan gudanar da sauraen.

## Saurare

TEA kan samar da jami'an sauraren bahasi da ba su nuna ɓangaranci don su gudanar da suararen. Jami'in da ke gudanar da sauraren ba ma'aikacin TEA ba ne ko wata hukuma da ke da dangantaka da sashen ilmi ko lura da yaronka sannan ba shi da kowane ra'ayi na ƙashin kai ko na aikinsa da zai yi saɓa ma manufarsa ko manufarta a yayin gudanar da sauraren. Jami'in sauraren bahasi: (1) Dole ya zama mai ilmi ya kuma fahimci tanade-tanaden IDEA, ƙa'idojin tarayya da na jaha akan abinda ya shafi tsarin IDEA, sannan fassarar manufar IDEA, daga kotunan jaha da tarayya; (2) Dole ne ya na da ilmi da ƙwarewar gudanar da saurare, ya kuma zartar da hukunci da rubuta shi, wanda yayi daidai ya dace, kyakkyawan hukunci na shari'a.

TEA kan kiyaye jerin sunayen jami'an gudanar da sauraren bahasi da suka ƙunshi ilmin kowane jami'in gudanar da saurare. Akwai wannan jerin bayanai a shafin yanar gizo na TEA a [Babban Ofishin Babban Mashawarci, Shirin Saurare na Ilmi Na Musamman (Kafa: bit.ly/2XCdKFw).](bit.ly/2XCdKFw) Kana kuma iya neman jerin abubnuwan a Ofishin TEA na Ayyukan Shari'a, waɗanda aka samar da bayanan tuntubarsu a ƙarshen wannan kundi.

## Kafin Saurare

Aƙalla kwanaki biyar na aiki kafin sauraren, dole ne kai da makaranta ku bayyanawa juna kowace irin shaida da za a gabatar a wurin sauraren bahasi. Kowane sashe na iya ƙin yarda da gabatar sa kowane shaidu da ba a sanar akan lokac ba. Haka kuma, aƙalla kwanaki biyar na aiki kafin saurare, to dole ne kai da makarantaku bayyanawa juna dukkan tantancewar da aka kammala a wannan wata da shawarwarin da aka dogara da su yayin tantancewar da kai ko makaranta ko shirin amfani da su a yayin sauraren. Jami'in sauraren na iya hana kowane bangaren da ya kasa yin daidai abinda aka buƙata daga gabatar da tantancewa mai alaƙa ko shawara a sauraren ba tare da amincewar wani sashe ba.

## A yayin Saurare

Kana da haƙƙi ka wakilci kanka a wurin sauraren bahasin. Har ila yau, kowane sashe ga sauraren bahasin (ciki har da saurare mai alaƙa da tsare-tsaren ladabtarwa) na da haƙƙin yin:

- Samun rakiyar lauya da/ko mutanen da ke da ilmi ko horo da ya shafi matsalolin yara masu fama da lalurori;
- Wakilci kansa ko wani lauya mai lasisin jahar Texas, ko wani mutum wanda ba lauya ba amma mai ilmi na musamman ko horo akan matsalar yara masu fama da lalurori sannan wanda ya cika ƙa'idojin da aka bayyana a [19 TAC §89.1175 (Kafa: bit.ly/2XFtKq9).](bit.ly/2XFtKq9)
- Gabatar da hujja da fuskanta, jarraba, da buƙatar halartar shaidu;
- Haramata gabatar da hujja a wurin sauraren da ba a bayyana ga kowane sashe ba cikin aƙalla kawanaki biyar na aiki, kafin sauraren;
- Samu a rubutaccen, ko, a ganin damarka, muryar sauraren da aka naɗa kalma-zuwa-kalma; da
- Samun rubutaccen, ko, a ganin damarka, binciken haƙika da matakan da aka gudanar ta latironi.

## Haƙƙin Iyaye Na Saurare

Dole a ba ka damar yin:

- Sa yaronka ya halarci sauraren;
- Buɗe sauraren ga jama'a; da
- Samun bayanin da aka ajiye na saurare, binciken haƙika da matakan da aka tanada maka a kyauta.

## Bayan Saurare

Jami'in saurare zai samar da mataki. Dole ne matakin jami'in sauraren kan ko yaronka ya samu FAPE ya zama an kafa shi bisa ƙaƙƙarfar hujja. Idan ka yi ƙorafi game da kuskure a tsare-tsare, to jami'in sauraren zai iya gano kawai idan yaronka bai samu FAPE ba idan da kuskure: an hana yaronka damar samun FAPE; hana yaronka more abubuwan da suka shafi ilmi; ko yin katsalandan cikin damar da kake da ita na shiga lamarin zartar da

abubuwa da suka shafi FAPE ga yaronka. Babu ko guda daga tanade-tanaden da aka ambata a sama da za a iya fassarawa wajen kare jami'in saurare daga ba makaranta umurni ta yi bi saharuddan da aka bayyana a sashen tsare-tsaren kariya na dokokin tarayya da ƙarƙashin tsarin IDEA Sashe na B (34 CFR §§500 through 300.536).

TEA za su tabbatar da cewa an cimma matakin saurare na ƙarshe sannan an aikawa sassan ta imel cikin kawanaki 45 na kalanda bayan ƙarewar wa'adin lokacin sulhu na kwanaki 30 na kalanda, ko akwai yuwar ƙara wa'adin lokacin sulhu. A cikin sauraren gaggawa, TEA za su tabbatar da cewa an cimma matakin ƙarshe cikin kwanaki 10 na karatu daga ranar gudanar da saurare. Jami'in gudanar da sauraren na iya yin wani takamaiman ƙari a bisa kyakkawan dalilli kan buƙatar kowane sashe a sauraren da ba na hanzari ba. Jami'in saurare na iya ƙin ƙarin lokaci a sauraren gaggawa. Matakin jami'in saurare (ya ƙunshi matakin saurare mai alaƙa da tsare-tsaren ladabtarwa) ya zama na ƙarshe sai fa idan sashe mai sauraren (kai ko makarantar) sau ɗaukaka ƙara zuwa kotun jaha ko tarayya, kamar yadda aka bayyana a ƙasa.

Dole makaranta ta aiwatar da hukuncin jami'i mai saurare cikin lokacin jami'in ya shata, ko idan ba a shata wani lokaci ba, cikin kwanaki 10 na karatu bayan ranar da aka yanke hukuncin, in ban da cewa kowane kuɗin aka biya da aka kashe a baya ana iya riƙe su har sai an daidaita. Babu wani da za da ke cikin tsare=tsaren kariya a dokokin tarayya ƙarƙashin IDEA Part B (34 C.F.R. §§300.500 ta hanyar 300.536 da za a iya fassarawa don kare ka daga shigar da wani koke na daban akan matsalar da ya ke daban da shirin sauraren bahasi da aka riga aka shigar.

### Ganowa da Hukunci zuwa Ga Kwamitin Shawara da Ɗaukacin Al'umma

Bayan goge dukan bayanan gane mutum daga hukuncin jami'in saurare, dole ne TEA su samar da hukunci (da ya ƙunshi sakamako binken da jami'in saurare ya gano da matakai) zuwa ga kwamitin shawara. A Texas, ana kiran kwamitin shawara na jaha Kwamitin Shwara Mai Ɗorewa. Dole ne TEA ya zartar da hukunci a gaban jama'a.

### Ɗaukar Matakin Sahri'a

Kowane sashe (kai ko makaranta) da bai yarda da sakamakon bincike ba da matakai ba a shirin gudanar da sauraren ba'asi (ciki har da saurare mai dangantaka da tsare-tsaren ladabtarwa) na da damar daukaka kara akan binciken da matakan jami'in ta hanyar daukar matakin shari'a a cikin ladabi kan cewa lamarin sauraren bahasi ne. Ana iya gabatar da matakin a gaban kotun jaha da ke da hurumin sauraren irin wannan sahiri' ko a gaban gunduma kotu ta Amirka ba tare da duba girman jayayyar ba sannan dole ne a gabatar da ita a kwanakin kalanda da ba su zarce 90 ba daga ranar da ka shigar da batun. A cikin bangaren dauaka ƙara, dole ne kotu ta samu bayanan da aka ajiye na sauraren bahasin, saurari ƙarin hujjoji yadda kowane sashe ya buƙata, bisa matakinta a gaban shaida, ya kuma bayar da saussaucin da ya dace.

Babu wani abu daga IDEA da zai rage ƙarfin ikon, tsare-tsare, da matakai da ke akwai a Amika. Kundin Tsarin Mulki, na Dokar Amurkawa Masu Fama da Lalura Ta Musamman na 1990, Taken Sabunta Dokar 1973 (Sashe 504) ko kowadanne dokokin tarayya masu kare haƙƙoƙin yara masu fama da lalura, sai fa ban da kafin shigar da ƙara a ƙarƙashin dokoki a neman sassauci da ke akwai a ƙarƙashin IDEA sannan aka bayyana a sama dole ne ya kasance ya yi daidai kamar yadda aka buƙataidan ka shigar da matakin a ƙarƙashin IDEA Sashe na B. Wannan na nufin cewa kana iya samun sassauci da ke akwai a ƙarƙashin wasu dokoki da suka saba da waɗanda ke akwai a ƙarƙashin IDEA, amma gabaɗaya, don samun sassauci a ƙarƙashin waɗannan dokoki, dole ne da farko ka yi amfani da sassaucin da ke akwai a ƙarƙashin tsarin IDEA, (wato, koken da ke kan ƙa'ida; shirin sulhu, ciki har taron sulhu; tsare-tsaren sauraren bahasi) kafin shigar da ƙara a gaban kotu.

### Kuɗin Lauya

A kowane mataki ko zaman kotu da aka gabatar a ƙarƙashin IDEA Sashe na B, kotun, a cikin tunaninta, na

iya bayar da kuɗin lauya na wani adadi a matsayin kudi gare ka, idan ka yi zarra (nasara).

A kowane mataki ko zaman kotu da aka gabatar a ƙarƙashin IDEA Sashe na B, kotun, a cikin tunaninta, na iya bayar da wani adadin kuɗin lauya ga makaranta ko hukumar ilmi ta jaha da ta yi zarra, da lauyanka zai biya, idan lauyan: (a) shigar da koke ko ƙara a gaban kotu da kotun ta sama maras dacewa, maras hujja ko maras dalili; **ko** (b) ci gaba da shari'ar bayan kuma sharia' ba ta dace ba, maras hujja, ko maras dalili; **ko**

A kowane mataki ko zaman kotu da aka gabatar a ƙarƙashin IDEA Sashe na B, kotun, a cikin tunaninta, na iya bayar da kuɗin da suka dace ga lauya a matsayin kudi ga makarantar da ta yi zarra ko hukumarr ilmi ta jaha, don kai ko lauyanka ya biya, idan buƙatarka na neman sauraren bahasi ko daga baya aka gabatar da shari'ar da ke gaban kotu akan kowane dalili na rashin dacewa, kamar hargitsa, haddasa jinkiri maras dalili, ko ƙarin kudi da babu dalili akan hukuncin ko zaman (saurare).

Kotu na bayar wani adadin kuɗin lauya kamar haka:

- Dole kuɗin su zama adadi ne da yayi zarra ga al'ummar da aikin ko sauraren ya taso akan inganci da kyakkyawan aikin da aka gudanar. Babu wata garaɓasa ko riɓanyawa da ake iya amfani da ita wajen zagayawa da kudin ba aka bayar.
- Kuɗin ba zai zama an bayar da su ba kuma ba za a bayar da wani adadin kuɗi ba a matsayin biya a cikin kowane hukunci ko zaman kotu a ƙarƙashin IDEA Sashe na B don ayyukan da aka yi bayan an ba ka tayi a rubuce na sassantawa idan:
    - An samar da tayin cikin lokacin da aka bayyana Doka ta 68 ta Dokokin Tarayya na Tsare-tsaren Jama'a ko, a cikin shari'ar neman saurare, a kowane lokaci fiye da kwanakin kalanda 10 kafin zaman ya soma;
    - Ba karbi tayin ba cikin kwana 10 na kalanda; sannan
    - Jami'in saure na kotu ko na gwamnati ya gano cewa sassaucin aka samu daga ƙarshe ba yi maka ba sosai fiye da tayin sasantawa.

Duk da waɗannan takurawa, bayar da kuɗin lauya da wasu kuɗi masu dangantaka da aka yi maka idan ka yi zarra sannan ka bayar da gamsasshiyar hujjar watsi da tayin sasantawa.

Kuɗin ba zai zama an bayar da su ba dangane da kowane taron kwamitin ARD sai fa idan an yi taron sakamakon zaman gudanarwa ko hukuncin ktu. Taron sulhu, kamar yadda aka bayyana a sama, ba a la'akari da shi a matsayin taron da aka kira sakamakon sauraren ko hukuncin kotu a dalin wadannan tanadae-tanaden kuɗin lauya.

Kotu kan rage, yadda ya dace, adadin kuɗin lauya da aka bayar a ƙarƙashin IDEA Sashe na B idan har kotu ta samu cewa:

- Kai ko lauya, a lokacin maganar hukunci ko zaman kotu, jinkiri maras dalili akan sulhu na ƙarshe;
- Adadin kuɗin lauya da a wani batu aka bayar da umurni a bayar ba bisa dalili ba ya zarce kuɗin sa'a-sa'a da ya dace da al'umma don ayyuka irin ɗaya na lauyoyi masu ƙwarewa iri ɗaya, da ɗaukaka da gogewa;
- Lokacin da aka shafe da ayyukan kotu da aka gudanar sun zarce la'akari da yanayin hukunci da zaman; ko
- Lauyan da ke wakiltarka bai samarwa makaranta da bayanan da suka dace ba a yayin shigar da koken kamar yadda aka bayyana a sama a sasen tsare-tsaren kariya.

Haka kuma, kotun na iya rage yawan kuɗin idan har ta gano cewa makaranta ko jaha sun yi jinkiri maras dalili akan sulhun ƙarshe na hukunci ko zaman ko aka samu rikici a ƙarƙashin tanadin tsare-tsaren kariya na IDEA Sashe na B.

**Hukuncin jaha mai alaka da shirin shiga tsakani na sauraren bahasi kan ilmi na musamman kan soma a [19 TAC §89.1151 (Kafa: bit.ly/3nQcmtG).](bit.ly/3nQcmtG)**

**An bar wannan shafin da gangan.**

## Bayanan Tuntuba

Idan kana da wasu tambayoyi game da bayanan da ke cikin wannan kundi ko neman wani ya yi maka bayani, sai ka tuntubi:

### Bayanan Tuntuba Na Cikin Gida

| | | |
|---|---|---|
| Makaranta:<br>Suna:<br>Lambar Waya:<br>Imel: | Cibiyar Ayyukan Ilmi:<br>Suna:<br>Lambar Waya:<br>Imel: | Wasu Manufofi:<br>Suna:<br>Lambar Waya:<br>Imel: |

Idan kana bukatar bayani game da lamurran ilmi na musamman, kana iya kiran Cibiyar Bayanan Ilmi Na Musamman a 1-855-SPEDTEX (1-855-773-3839). Idan ka kira wannan lamba ka bar sako, wani zai kira ka ranakun aiki. Mutanen da suke kurame ne ko masu lalura ji na iya kiran lambar SPEDTEX ta amfani da Relay Texas 7-1-1.

Idan kana da tambayoyi game da jiran koken da aka shigar akan ilmi na musamman, sai a kira 512-463-9414. Idan kana da tambayoyi game da jiran shiga tsakanin ko shirin sauraren ba'asi, tuntubi mai shiga tsakani da aka saka ko jami'in sauraren bahasi a lokaci daya.

## Bayanan tuntubar Sashen Sulhunta Jayayya

| | | | |
|---|---|---|---|
| A yayin neman Shiga Tsakani, aika bukatar zuwa ga:<br><br>**Gudanar Da Tsarin IEP Na Jaha**<br>Hukumar Ilmi ta Texas<br>1701 N. Congress Avenue<br>Austin, TX 78701-1494<br>ko<br>Fax: 512-463-9560<br>ko<br>specialeducation@tea.texas.gov | A yayin shigar da Koken Sauraren Bahasi, aika da koken zuwa ga:<br><br>**Koke akan Ilmi na Musammans Sashe**<br>Hukumar Ilmi ta Texas<br>1701 N. Congress Avenue<br>Austin, TX 78701-1494<br>ko<br>Fax: 512-463-9560<br>ko<br>specialeducation@tea.texas.gov | A yayin neman Shiga Tsakani, aika bukatar zuwa ga:<br><br>**Jami'in Gudanarwa Mai Siga Tsakani**<br>Hukumar Ilmi ta Texas<br>1701 N. Congress Avenue<br>Austin, TX 78701-1494<br>ko<br>Fax: 512-463-6027<br>ko<br>SE-Legal@tea.texas.gov | A yayin shigar da Koken Sauraren Bahasi, aika da koken zuwa ga:<br><br>**Shirin Sauraren Bahasi Na Ilmi Na Musamman**<br>Hukumar Ilmi ta Texas<br>1701 N. Congress Avenue<br>Austin, TX 78701-1494<br>ko<br>Fax: 512-463-6027<br>ko<br>SE-Legal@tea.texas.gov |

**Sai a ziyarci sahfin yanar gizo na Sashen Ilmi na Musamman na TEA**

https://tea.texas.gov/TexasSped